IKI book 4 part 1
ZURFIN CIKI book 4 part 1
Posted by Bashir Sani Fesan on 15 Dec 2016 - 00:42
Inna harira tace, Allah ya kyauta ku tashi mu tafi. Suka mike Suka nufi dakin ummi. Duk da ummi a da bata tunanin tana da lokacin bishira, yanxu kam dole tasan zaman da zasuyi. Su inna saratu suka ce ma ummi duk abinda zatayi don allah kada ki kulata. Suka ce tayi harkokin gabanta tayi biyayya wa mijinta shine abunda zai fisheta. Ummi tace To amma a zuciyarta bata tunanin zata zuba ido a rainata. Suna tafiya fatima ta shigo yiman sallama, ummi tace don allah fati ki dan tsaya ni kadai fa zan zauna a dakin nan. fati tace wayace kada kisan kawaye? Ummi ta ce wane kawaye, auren da a ka daura cikin yan mintina? Fati tace, Yau zakiji abinda mata kaji. Ummi ta damko mayafin fati, ni fa inajin turo, wai da gaske da wahala ko kina tsokanata ne? Fati ta kamo kunnen ummi tayi mata rada. Ummi ta zaro ido tare da cewa, Da gaske? Fati ta sheke da dariya tace sai nazo jin batun. Ummi tace sirrine ya za'ayi in fada miki sirrina? Fati tace au ni shine na fadamaki nawa ko? Ummi tace kinyi haram da kika fada fati tace, "ke kuma kinji haram ko? Suka sa dariya. Duk yanda ummi taso fati ta tsaya amman taki, don haka sukayi sallama. Fati ta shige dakin bishira don yi mata sallama. Bishira tace, fati fitar min daga daki bana wasa dake, tunda kema naga kin koma jam'iyar waccan yar iskar, fati ta fita, cikin ranta tana cewa ba zanki yar uwata ba don kishinki na banza tayi tafiyata. Ummi tsuru tayi tanaji tsoron abinda fati ta fadamata, amman sai wata zucia tace keda ba sonki yake ba kila ma bazaibi ta kanki ba, sannan ta samu yar natsuwa. Abba ya fito zai nufi gida sai kuma ya fasa ya nufi super market, ya siyo audugar mata yana tsammanin gobe ne zata tashi da al'ada a lissafinsa. Tun sanda ta soma bai taba mance ranar ba, haka in ya chanza mata lokaci duk yana lissafe. Ya sai masu yan kayan masarufi sannan ya fito, gida ya nufa amman gabansa yana faduwa kila har

yanxun ba a kai ummi ba. Da yayi fakin sai kuma ya nufi gidan su umma duk kowa ya watse. Yayi sallama tsohuwa tana alwala ta amsa. Umma daga kicin ta amsa, tsohuwa tace "wane kinibibin kuma ya kawoka mai sunan malam? Bayan an kai maka ita? Yace kaji tsohuwa da wata magana da gurin ummi nake zuwa? Ni gidan mu ne. Tace kadaiji shi, takwara dai kada inji kada in gani, don nace mata duk abunda kuka mata tazo ta fadamin. Yarinyar nan tana kuka wiwi tabar gidan nan. Umma cikin dariya tace "toh ai tsohuwa in don Abba baza ayi fada ba, ummin ce dai abin jama kunnen. Tsohuwa tace 'a' a daina zancen nan suwaiba kada ma ya samu nayi. Abba yace" Toh bari in zo in hada maki kayanki mu tafi can don kada wani ya zafin cewa. Kinga kyafi tare mata. Tace ina gana nan din ma zanji. Yace Alhaji sun shigo kuwa umma? Tace A'a basu shigo ba. Yace toh bari in isa gida. Tace toh Abba ummi ma dazun aka rakata. Don allah Abba ka kara hankuri a kan na da, sannan matarka kuma kada kace zaka nuna mata bambanci a kan ummi yar uwarka ce. Ka kwantar mata da hankali ka mata adalci, sannan kada ka bawa ummi kofar da zata raina bishira. Yace zan kiyaye insha allah, kuma don allah umma ki kara mika godiata gurin alhaji. Tace haba Abba yaya kake fadin haka? Alhaji ai mahaifinka ne karka dinga kallon alakarka da ummi. Yace haka ne duk da haka dai a min godia, tsohuwa tace yaki godia ya samu mata a sama don rashin imani mai sunan malam ko gyauto bai sa mata ba, toh kasani tana binka bashin lefe. Abba Yace umma ni dai na wuce. Umma cikin dariya tace "Toh Abba. Yace tsohuwa ni nayi gaba, don in na cika tsayuwa a nan kila mu dambace, Tsohuwa tace kai dai jeka na baka amana ya tafi yana dariya. Koda ya kai kofar gidan sai ya bude mota ya dauki kayan masarufinshi ya nufi cikin gidan salam dai duk da jarumta irin tashi gabansa ne ke faduwa. Bai san wace irin masifar bishira ta tanada ba. Ya shiga da sallama. Bishira tana zaune akofar daki tana goye da muhibba, amman bata amsa ba. Duhun

magriba ya soma dan daf da a kira sallah a ke, yace bishira ya ba a tada inajin ba? Tace tunda kazo yanxun ai sai ka tada kai. Da kafin wata tazo ai baka taba zuwa kace a tada inji ba. "Abba ya kalleta a zuciyarshi Yace" mata kenan masu manta alhaji. Ya aje ledodin hannunshi ya nufi injin. Bishira ta mike ta nufi ledodin tana fadin Tun yanxu a aka shigo mata da kazar, alamun ba za'ayi ada ba kenan. Ni lokaci na sa wuraren tara ya shigo ina lissafe da komai, ta bude ledodin sai taga kayan masarufi d kuma audugar mata. Tsaki taja tare da dangwarar dasu yana kallonta da ya kara mai ya tada injin sa yazo ya kwashe ledodin ya shiga falonta.vels / ZURFIN CIKI book 4 part 2

ZURFIN CIKI book 4 part 2

Posted by Bashir Sani Fesan on 15 Dec 2016 - 00:44

Kujerun da aka chanza mata masu kyau, amman a ran abba yace ya basu sati biyu. Ya cire riga ya fito yana son yayi wanka ne kafin a kira sallar magana,yaja ruwa da sauri da sauri yayi ban daki ya fito ya shiga falo ya kwalama bishira kira. Tace minene kake damuna? Yace ina aka kai min akwatuna na? Tace tace ina kuwa gasu can a kicin da sauri ya fito, kicin din lafia? Ya tsaya yana kallonta bani da mutuncin da za'a sa min kayana a daki? Tace ni da aka guji dakina da kayan a kace ni kazama ce, me zaisa in sake kaine? Daga baice komai ba ya nufi kicin ya kwaso akwatuna shi da takalmin shi ya kai falonta. Bai tsaya chanza kaya ba, ya nufi masallaci don zai rasa sallah. Bai baro masallaci ba sai bayan isha'i amman bishira tana zauna. Ummi kam ta kasa fitowa don tana kyankyamin ban dakin, gashi al ada ta sameta da yamman nan, sannan duk tanajin abin da sukeyi da matarshi. Ya shigo gidan ya chanza kaya sabi fil, ya feshe jikinsa da turarukkanshi wayar shi ta soma ringing ya daga salis ne. Yace aboki in ba sallama akwai daga hannu ko? Kace an kai maka rabin ranka koda ba zamu rakaka ba ai kayi mana sallama. Cikin dariya Abba yace na yafe salis yace To Allah ya bada zaman lafia. Suka yi sallama zai aje wayar kenan sako ya shigo. Ya

duba ummi ce da wayar nan da ya bata ajiya cewa tayi, ina da matsala, ina bukatar taimako. Gabanshi ya fadi, sai kuma ya tuna kila al'adar ce, don haka sai ya saka hularshi ya dauki ledar audugar ya nufi dakinta. Har lokacin bishira nan zaune inda take, tace au tun daga yanxu za'a soma rashin adalcin? An dauki leda an nufi dakinta? Sam baiko waiwayo ba, yayi sallama ta amsa tare da gyara mayafinta, ya shiga suka kalli juna Cikin ido zukatansu sukayi fari kal. Cikin taushin murya yace, wane taimako kike bukatar? Ta lumshe ido sannan ta juya masa baya domin kunya ta rufeta. Yace To karba ya mike mata ledar ta waiwayo ta ansa da hannu biyu. Mamaki ya cikata ganin audugar, ya yayi har ya san tana bukatar audugar kuma a ina yake sanin lokacin al'adarta har idan ya chanza? Tace nagode yayi dan murmushi nima ina godia. Ya juya har ya daga labule tace "Em na ce....." ya waiwayo yace kika ce mi? Tace don allah inason maganin wanke bayi ne, tayi maganar Cikin kyankyami, sakamakon irin dattin da tagani a bandaki tare da gamsa kuka. Yayi murmushi wane iri kikeso? (IZAL) yace ai akwai amman yanxu Bai kamata ki shiga wankin bayi ba. Tace zan wanke in dai akwai. Yace bari in wanke maki, da sa tace a'a yaya Abba zan wanke. Falon ya koma ya cire rigarshi ya shiga jan ruwa. Bishira tana zaune ta mike ina badai abokitaina ba, in zaka kwashe mata rijiyar kwashe, amman a juye ko in baras kuma in dai ruwan da za'ayi amfani dashi ne kakeja, To kesani nima duk lokacin da zanyi amfani da ruwa saika dibar min, ehee. Ummi ta fito da bokitai don duk tana jinsu, tazo wurin Cikin sanyin murya tace, Ya Abba don allah ka bari in ja ruwan nan. Ya kalleta, take ya manta da duk bakin Cikin da bishira ta kunsa mashi. Yanxun daga zuwa saiki fara jan ruwa? Ummi tazo ta kama igiyar gugar, ai ba zama nazoyi ba, Ya Abba bauta nazo yi, Aljanna sai an dage. Ya saki dariya bishira ta dakatar dashi da ce wa "Karuwanci za'a gwadaman? Ta daga ruwan da ya zuba a bukati zata watsama ummi, yace kina

watsa mata zan baki Mamaki. Cikin tsawa yayi maganar ta tsaya cak da bokitin yace, Sakarya mai kishin hauka. Yaci gaba da jan ruwan yana zubawa abokitan da ummi ta fito dashi. Bishira ta aje ruwan sannan ta hankadar dashi a kasa, Bai ko kalleta ba. Ya zuba ruwan sannan ya fito da izal da omo. Daki ummi ta koma ta dauko tsinsiyar da aka sai mata don wankin bayi, kin tafiya Abba yayi tana wankewa yana zuba mata ruwa har sai da taga bayin yayi yanda take bukatar sannan ta hankura. kyankyami jikinta takeji don haka taje ta hada kayan wanka har lokacinzurfin Ya Abba yana wurin rijiyar. So take ya matsa taja ruwan amman yaki, don ya lura bishira shi kadai take shakka zata iya zartar da komai kan ummi. Shine ya sake zuba mah ummi ruwan wanka, sannan ya coge har ta gama ta fito rufe da hijabi tayi dakinta, sannan ya dauraye jikinsa yaje ya maida kayanshi ya nufi wane. Bishira tana nan wurin kofarta ta kasa zaune ta kasa tsaye, bakinta kuma Bai fasa sambatu ba sai kace sabon kamun hauka. Fadi take kuma a zo a biyani duk basisikan da nike, ehee. Kuma in yarinya tamin in murji bukina. Ummi kam ta gyara jikinta tsab ta saka sabbin kaya ta feshe jikinta da turarokan da umma ta sai mata. Tunda ba lefe aka mata ba bare ta samu kayan shiga. Kan doguwar kujera ta mike, salam yanzu taji yinwa tana tsammanin rabonta da abinci tun karin safe. Ta shafa Cikin ta ina ma umma na aiko man da abinci. Ta furta a fili WAYA nan ta jawo tana tunanin sanar da Abba cewa tana jin yunwa. Sai wata zucia ta hanata wannan ba girman amarya bane. don haka ta share ta bude shafin game tana ta bugawa. Sai sha daya Abba ya shigo gidan, ya rufe gidan. Nufinshi ya wuce kai tsaye dakin ummi, amma sai ya tuna da kazar da ita bishira ya sawo mata. Duk da baya tunanin ta karba ga mamakinsa tana tsaye a tsakar daki har yanxu da daurin kirji take. Wannan ya nuna batayi sallah ba, bare wanka. Ya mike mata wata harara ta zabga masa banaci, ya juya batare da yace mata kala ba, ta biyo bayan shi, A bani

basussukana da nike bi malam. Ya nufi dakin ummi taba biye dashi, ummi ta turo kofa dama yana kokarin tura kofa dama yana kokarin tura kofar bishira tana rike masa riga ta baya. Ya waiwayo Cikin zafin nama zai wanka mata mari sai taci sa'a ta tsugunna, Cikin azama ta yunkura tayi baya da gudu. Banda tsaki da yaja Bai ce komai ba. Ya shige dakin ummi da sallama, ummi bacci ya dan dauketa saboda gajiya. A kan kujera take da waya a hannunta. 4rm Shamsy bello balarabe.IKI novels / ZURFIN CIKI book 4 part 3
ZURFIN CIKI book 4 part 3
Posted by Bashir Sani Fesan on 15 Dec 2016 - 00:48
Niyyarta yau sai taji komai, don haka ta kai yarta ta kwantar, dai dai lokacin ne abba ya fito don kashe injin. Sake fitowar da tayi ne taganshi zai koma. Wayan cewa tayi da daukar buta ta shiga bandaki, shi kuma ya shiga daki ya kulle kofa, tazo ta manne jikin kofar. Fitar abba shine yaba ummi damar saka kayan baccinta, don bata iya bacci da kaya masu nauyi. Fargabarta yaya kwanciyar tasu zata kasance? Kan kujera ta zauna tare da kwantar da kanta a hannun kujera. Shima abba yana da jin zafi don baya iya bacci da kaya sai da gajeran wando kurum, idanu ummi ta kulle lokacin da taga ya abba ya soma cire tufafinsa ga hasken cocilar da ya kunna. Filo ya dauka ya jefa Kan doguwar kujera ya kwanta rigingine, ganin haka sai ummi ta mike ta nufi gado addu'a tayi sannan ta lumshe ido har bacci ya dauketa. Fuskarta cike da murmushi zuciyarta cike da godia allah yau gata dakin ya abba a matsayin matarsa. Abu daya ya rage mata shine ta koya masa yarda zaya sota. shima farin ciki ne a ranshi yayi da idanuwanshi sukayi kuri a Kan gado yana hango ummi ya ta zama halalinsa Abu daya ya rage shine ya koya mata sonsa. Bishira data labe bata jiyo komai amman kunnuwanta suna jiyo mata magana kasa kasa,,hawaye na zuba a idonta batasan iya adadin awanin data dauka a kai ba. Koda ta koma daki juyi kawai take a gado. Abbanta abun sonta yana can kwance da wata, watar ma makiyiyarta wadda ta

tsana. Wata zuciya tace kije ki watsa masu man petur wata tace ki bari da safe ki caka masu wuka babu abinda bata rayaba har asubahin farko. Labule ta daga ta shiga leke taga ko zasu fito, lokacin ne kuwa abba ya fito yaja ruwa a bokitai yayi wanka da alwala. Ba zata gane ko wani Abu ya faru tsakaninsa da ummi ba don wanka al'adarshi ce Koda bai dauki najasa ba. Nafila ya shiga yi da rokon allah yasa ummi ta so shi, ya kuma hada masa kansu. Koda zai tafi masallaci bai tashi ummi ba tunda yasan ba sallah zatayi ba. Bishira ta fito tasa kujera kofar daki ta zauna, saboda tashi bai bar ummi bacci ba, don haka ta tashi in tana al'ada yini take wanka gaba daya sai ta tah ktankyamin jikin ta. Ta fito da bokitai duk ta cika d ruwa, Bishira tana kallonta sai da ta wanke bayi tas, sannan tayi wanka. Sauri take tayi kwalliya don a cikin nasihohin da umma tayi mata a safiyar da za'a kawota gidan miji tace kada ta sake mijinta ya ganta cikin kazamin yanayi. Kuma kada ta bari ya shaki wari daga gareta, tayi shafe shafenta. Atamfa ta saka riga da siket mai ruwan hoda hoda da ruwan kwai. Daurin dan kwali ta kafa sannan ta feshe jikinta da turaruka masu kamshin gaske, sannan ta shiga gyaran dakin duk da ba datti yayi ba. kayan da abba ya cire ta ninke don da jallabiya yake zuwa masallaci, sannan ta dau kujera ta kishingida saida gari yayi haske sannan ya nufo gida. Tsaki bishira ta jamashi maimakon amsa sallamar ta kara da cewa an girma ba'a san an girma ba, an kwana da yar ciki abin kunya. Ai wallahi baka cika dan halas ba da ka auri yarinyar datayi sanadin kulleka kaci duka har aka ballaka ba. Ya kalleta dalilin kenan da ban cika dan halas ba? Tace eh baka cika ba, yace toh jeka naji ni shege ne, in don dai na auri ummi ne, tace munafuki dama can kana sonta. Ya sake wai wayoowa yace so kuwa mai tsanani. Takaici ya cikata ta daga murya allah ya isa munafuki. Ya nufi dakin ummi wadda ke sauraren duk abunda ake. A cikin ranta tace ina ma son da gaske ne? Tasan ya fada don kawai yaba

matarsa haushi. Da sallama ya daga labulen, ummi ta amsa tare da tashi daga kishingida da tayi, ya zauna tare da lumshe ido. Lokacin daya kuma ya shaki kamshin turarukan data fesa. Ya kalli Fuskarta labbanta da yake matukar so sun sha jambaki ruwan hoda. Take abba ya manta da duk wata damuna koh kalma marar dadi da bishira ta fada masa. Daga inda take zaune ta dan rankwafa don girmamawa tace ya abba ina kwana? Lafia qalau ummin abba ya bakon wuri? Ta lumshe ido saboda jin dadi sunan daya fada mata. Alhmdllh ya sake karkatawa yana kallonta sosai yace to masha allah, yanxu kinsan minene? Ta tattara hankalinta gareshi tace a'a? Yace kiyi hnkr nasan a al'adar ta hausawa amarya ta Kan yi sati daya cir ba tare data yi ko cangal ba. Toh hnkr zakiyi kinga ke tun daga kawoki jiya kin soma da wanki toilet. Sannan yanxu ma ina son ki ciro rishonki a hada shi a sa kalanzir mu karya. Kin dai ga yanayin yanda matar gidan take gudanar da nata kishin. Ummi ta gyara zama ta tuna nasihar ummanta da tace in zaki yima mijinki magana kalaman ya zamana kin zabo su ne ba wai kin sakesu ba. Ta kalle shi, shima ita yake kallo, tace ya abba don wannan ne kake ban hnkr? Yayi murmushi tare da lumshe ido ya kuma budesu lokacin guda, a yaran soyayya yana nufin eh, itama ta fahimci yaren don haka taci gaba da cewa. Ya abba ni dama ba zama nazo ba, neman aljanna nazo kuma zanyi komai don na sameta. Don haka kadaina bani hnkr umurni kawai zaka bani. Tun daga tsakiyar Kan abba har zuwa babban yatsansa sai da ya motsa, don sanyin muryar da ummi tayi amfani da ita tare da kyawawan kalaman ta. A zuciyarshi yace tabbas ummi haihuwar ummanshi ce, duk rainon umma dole zai zama daban ciki ya'ya. Ya kalli ummi allah yayi maki albarka tace amin. Ta mike ya bita da kallo taje gurin da a ka shirga mata kayan aiki ta zakulo risho yace to muje kicin dinZURFIN CIKI book 4 part 4

ZURFIN CIKI book 4 part 4

Posted by Bashir Sani Fesan on 15 Dec 2016 - 01:13

Ta mike ya bita dkallo tje gurin da aka shirge mta

kayan aiki ta zakulo risho yce to muje kicin din. Tkarya murya, ya Abba amin afuwa, bna son in shiga kicin din can kmin hakuri insa rishona akofar daki. Ykalleta, bazai tkura mta ba domin ysan duk wnda yzauna da umma dole zai zama me kyankyani, yce indai zai miki kiyi kawai , in na smu ynd da nke so dga baya sai ayi miki kicin a gurin, tce ngd. Shi kan da kanshi yfito darisho yn budewa ya hadashi, tafito da tukunya tanufi rijiya, ta dauraye sannan tazubo ruwa.Bishira kuwa dma tazo talabe duk tji maganganun dsu kayine, jin abba zai fito da risho sai ta gudu daki. Sintiri ta dinga yi tna magana ita kadai, wato abban walid nece mazai ce anga irin nawa kishin? Yarinyar dya ce bsonta yke ba dole akayi masa shine har ysoma kai mta gulmata. Har dawani shi mata albarka , tunda uwarta ta kitso mata ynda zata ce ai dole yashi mta albarka, to ni ya tsine min kawai. Ummi ta amshi galan din kalanzir din dga hannunshi tre da cewa ya abba kawo inzuba zai ce ta barshi kenan wayarshi ta soma ruri, yadaga. Anty ce, suka gaisa tce tna son yin magana da bishira ya mike ytafi kaimata ummi kam ci gbata yi dasa kalanzir dinta takunna rishon tdora ruwan zafinta takoma daki, shima yna bt wayar ydawo. Anty tce bishira dm na kira kine inji bakuwar dta kwana a gidan da safennan kin bta abin kari ko? Bishira tahade rai tamkar tana gabanta, anty tome mexan bta, ina ruwana ma da ita? Dazunnan fa suka gama gulmata wai har yna ce mta tye hakuri tdai ga irin mtar gidan. Anty tce hauka kike tyi shi ysa ai dole yce haka. Ynzun dai sai ki tashi kibsu abin kari, hka da rna. Karki sake yarinyar nan ta dora tukunya sai byan sati daya, kina jina ko? Bishira tace to bdan zancan ykai ranta ta amsa ba. Sai don tunanin kada zancan zuwa makkanta yafasu . Sunayin sallama ta aje wayar tre da cewa, koda uwarta tke ywo bzan dfa mta abinci ba. Sai da ummi ta wanke flas din shayin sannan tazuba ruwan, falon bishira yje ydauko kayan shayin dbiredi. Tace, itama kakai mta ruwan zafin. Yce ta dafa, ygama yashirya tsaf don zuwa gurin aiki, harbakin kofar

daki tarakashi. Yce, ummi naroke ki koda bishira tna zaginki ne don Allah kda ki kulata, sambana ganin laifinta don nasan sboda sona tkeyi. Nan da wni lokaci komai zai daidaita. Ummi tce kada kadamu insha Allah ba abin dazai faru, allah ya tsare yace amin nagode. Dakin bishira yaleka ya amshi wayarshi, sannan yce mezakuyi drana? Tzabga mishi harara, ina ruwana dawani abinci. Ya aje mata dari hudu. Gashi kusai nama nasan akwai komai ko? Tsaki taja, gara maka dauki kudinka don bzan dafa ma munafukai suci suji dadin zagina. Yakalleta, Allah yganar dke. Tdg murya yganar dakai dai maci amana sainaga bayanku. Bki yataba kafin yafita, baice mata kala ba. Ummi ta kinkimi akwatinan kayan abba dya kawo mt tgyara msu mzauni, sannan takwashe 'yan kofunan dasuka sha tea ta wanke. Sannan takoma dki tna jin wsu kawayen bishira sunzo sunata habaice dazage-zage, ummi bt fito ba bare ta tanka. **** **** Bashir abin duniya ya ishe shi, ykasa sukuni sbd son ummi, yzuga ummanshi sun kai suka gidan su sahabi don afasa auran anfasa kuma duk da hk ummin tzama btashiba. Jinshi yke tamkar ykashe abba don tsana, don hka koyaushe cikin zuga umma yke dan kawai tatsani Abb. Guraran sha biyu ummi bacci yasoma dibanta sai tji muryar umman bashi akofar dakinta tna cewa ina ummin tke munafauka, fitsararriya tadaga labulan kofar tarike. ummi takalle ta. Kin kalle mi mna 'yar makirai. Kin bar smun zman lfy a gidannan, kuma uwarki ko tn tsafi dbakin kare dbakin dodo sai kinbar gidan dana. Ke inzan tafi dazani daya mtsawar bokaye da 'yan bori suna nunfashi kin smun nutsuwa agidannan. Bishira tace, umma shima munafuki ne shida yce bai sonta amma dazun haryi dni sukayi. Umman bashir tce shi Abba kimasa uzuri, duk abinda ykeyi byin knshi bne, anriga an rikita shi, bakya ganin shi duk afirgice yke? 'yar bori tafada min komai, ynzun karya tambaya muke nema. Bishira tce duk dhaka ma ynso, ai ance asiri yan tarad dahali. Umman bashir tce hk ne, shi dinma ai ubansa zaici ba

dagin kafa. Ummi datna zaune kai duke, sam zantukansu bsu dme tba, abu dya yagirgizata btun asiri. Bta son ashiga tsakaninta da mijinta tun kafin su fara son juna. Saidai kuma dta tuna da addu'o'inta da takeyi bta fsa yi ba. Ga Azkar safe dayamma, saitasamu ntsuwa tsan Allah
yafisu.ovels / ZURFIN CIKI book 4 part 5

ZURFIN CIKI book 4 part 5

Posted by Bashir Sani Fesan on 15 Dec 2016 - 01:33

Umman bashir tagama jarabarta tafita, karfe daya drabi Abba ykira wayar dke hnnun ummi tdaga. Cikin girmmawa tce, snnu da aiki ya Abba, ina ftn kn cikin koshin lpy? Yyi murmushi cikin jindadi yce, lpy nke ummi, am...in... Dama zan cene kin ci abinci? Tce A'a, amma bna jin yunwa, dnaji yunwa zn sha tea ai, kda kdamu kai fa kci? Yyi dan tsaki, tsiyar bna cin abinci awaje ummi, abincin umma kdai ke min dadi, Allah ys zki gjeta. 'yar driya ummi tayi, insha Allahu sai mna fita. Yce anya kuwa? Tce insha Allahu ai nace. Kin gma mgna yafadi tre dyin murmushi mai sauti, yawwa bari in kirata ta turo miki da abinci, tce to ngd. Yce, nima na gode, sai ndawo. Tce, to Ya Abba kdawo lpy, ka kula min dkanka. Tkashe wayar, yjima yna kallon wyar tre dmamakin ynda ummi ta iya zantuka masu kwantar dahankali, irin wdanda bishira da ta ba ta shekaru bta iya ba. Ykira lyin ummanshi suka gaisa, yce ummana don Allah kitura ma ummi abinci, umma tce, kan wani dlili Abba? Tci gba dacewa, tbdijam!, bza ayi hk dniba. Abba ymarairaice murya, don Allh ummana yunwa tke ji. Umma tce, ta tashi tdora mna? Abba tsaya kaji, dadai wta ce can kke aure ba ummi ba sai na aika mta, amma ynzun ga uwargidanka agidan shi kenan sai in aikamata da abinci? Wannan ba gsky bne, sannan zgin da ake min ai sai ya linku yfi nada, yce umma duk wnda yzageki rshin fhimta ne. Kuma fana baiwa bishira kudin cefane amma tki tdafa musu abinci, tce kila tgaji ne, shiyasa bta dfa ba. Ita ummi dba saita amsa tdafa musu ba? Yce, amma dai umma tsakani da Allah kowacce amary bsai ta kwana 7 bsannan tke fara dfa abinci? Umma tce, ai ba

addini bne al'ada ce, don takama girki ai ba laifi tyi ba, yce, shikenan umma tunda kin hna sai anjima, tce mujima dayawa. Shiru abba yyi yna tunanin mgangnun umma, ysan gsky tfada, amma dmuwarshi ummi dbta ci komai ba. Ykalli agogo, saura kusan awa 2 ytashi, wayarta yske kira, tdaga yce ummi kisha tea din umma bta da abinci kfin ndawo. Tce, to ya Abba, kkusa dwowane? Yce, sai nan da awa 2. Tce to Ya abba, sai ka iso. Bta wni sha tea bdon bta jin yunwa sam, tshi tayi tasake kakkabe dkinta don mutane suna tshigowa ganin dki yra dmanya. Tas tkakkabe ko ina tafito tshare tsakar gidan lungu dasako, bishira lokacin mbata gidan wsu yra dsuka shigo tbasu kasko suka smo mt rushi tzuba turaren wuta mai kyau dkamshi. Tnayi tn kallon agogo, saura minti ashirin yaya Abbanta ydwo ta wanke byi tsake wnka, sannan tdibar masa ruwan wanka shima ta aje akofarta. Trufe kafin ya iso, tshiga dki tna ta shafe-shafenta, sai lokacin bishira ta shigo gida. Tna rike da 'yarta akafada, ita kanta 'yar ba amata wanka ba bre uwar, tkwabe hijabi trataye, sannan tzauna akofar dakin tna kallon tsakar gidan. Duk da ita knta gurin ybta sha'awa, amma bki ta taba tre dcewa, wahalalliyar bnza. Ummi tayi mtukar kya cikin wando da riga nawani ydin dshi Abba ydinka mta a babbar sallar dta gbata. Tasaki gashinta sosai tyi wani daurin dankwalin da ita ce ta iyashi amma gshin nta duk yna wje. Tfesa turarukanta sannan tfada kan kujera, tkalli agogo minti goma takaru akan lokacin dya fada mta. Zuciyarta tdan dmu tkosa sosai ta gnshi bta ki yzauna agida tyi ta kallonshi tre da sauraron muryarshi ba. Sai dkusan minti 20 sannan Ya Abba yshigo, tsayawa yyi yna kallon tsakar gidan, yau kam farin cikine ya mye gurbin bakin cikin dyake ji aduk lokacin dya shigo gidan ykalli tsakar gidan. Kamshin irin turaren wutan da umma ke cika gidanta dashi ne yke shaka. Ysaki murmushi tre dyin sallama, bishira dke zaune dabas atsakar gidan maimakon ta amsa sallamar sai tsaki taje dogo tre da cewa. Aikin bnza. Kallonta kurum yayi ranshi ya baci.

Bai cemata kala ba ynufi dkin ummi, tyi nisa cikin buga game. Sallamarshi ceta sata yin jifa da wayar akan kujera tamike tdaga labulan daidai lokacin dyke cewa inshigo? Ta amsa sallamar dwata murya wadda bta san ma tna da ita ba, suka kalli juna cikin ido, lokaci 1 suka ski murmushi tmika hannu kafadarsh rtaye da wta jaka wadda bda ita yfita ba. Ya salubo jkar ymika mt tre dcewa, kirike dakarfi, tce to, sannu ddawowa. Yshigo rike da leda ahannunshi yzauna tre dcewa. Yauwa, tnufi robar ruwa data dauraye jug din data tnda don shi kadai, tzubo ruwa tzo dakofi tadauraye kofin snnan tzuba ruwan tmika msa tre dsake cewa, sannu dkokari. Ydubeta, yauwa kema sannu dkokar, dud da byajin kishi dole ne ysha ruwan, ybude bki ysoma shan ruwa. Sai yaji ruwan yfi duk wani ruwa dyasha a tsayin rayuwarshi gardi dkuma dadi, ydubeta ido lumshe dama ruwan amare dadin shi dabanne?? ZURFIN CIKI book 4 part 6
Posted by Bashir Sani Fesan on 15 Dec 2016 - 01:37
Ta kyalkyale da dariya, ya Abba yayi santin ruwa, yyi murmushi, naji ne kman kinsa zuma, ya cire takalmashi tre ddora kafafuwanshi akan dan teburin da aka aje don dora abinci ko kofi. Tazo takwashe tkalman tkaisu kusa da kofar fita tyi musu ajiya mai kyau, sannan tadauko dan twul tshare kasar gurin. Ykalleta, yi hkuri nshigo miki dki datakalmi ko? Tce bkomai aranshi yce nsaba shiga dakin bishira da tkalmi. Yjanyo ledar dya shigo da ita tre dcewa ummana tki aiko miki da abinci ko? Tace, kyi mta mgnane? Ya ciro take away din yasiyo mata, zo kici, ai dole ta bmu na dare, zan jene in tsaya mata. Ummi tdubeshi, anty bishira fa ka bata nata ne? Yyi mta banza, tduba ledar tga guda daya gakuma wnda yciro mata. In kaima anti bishira? Ydaka mta tsawa tre dharararta, ke! Ban aike kiba, tatsaya tna kallonshi, meye ruwanki da mtata, kin fini snin meye kamata nayi kenan? Yja dogon tsaki tare djanyo jakar dta dora mishi akan gado, jikin ummi yyi sanyi. Ta tuna damaganar da umma acikin nasihar dta mta, kda kizama dga cikin mtan dsuke btawa mzajensu rai. Hakan yna sawa miji

yatsani matarsa, kiyi tka tsantsan kinsan hlin abba yna dsaurin fushi. Dsauri ummi tasulalo dga kujera. Don Allah kyi hkuri ya abba, ban san zakaji haushi ba. Ydubeta fuska daure, hwaye ygni sun cika idonta yace, kda ki sake hawayen nansu zubo, tsa ytsunta tdanna idnunta, tshi ki zauna ki dauki abinci kici. Tzauna tarike abincin tkasa ci. Ykalleta suka hda ido cikin ido, tariga shi mgna kayi hkuri Yaya Abba, tausayinta ykamashi amma sai ydake. Bnason kisake mgna akan abinda yshafi mtata kinji ko? Da sauri tce, bzan kra ba. Yyi dan murmushi ci abincinki. Tasauke wta irin ajiyar zuciyar dhar ya klleta da ido ya tmbayeta lpy? Dabaki tfurta lpy lau, yce ci abincinki. Ummi tdauki abinci tn ci, jefi-jefi tna kallonshi, shi kuma yna ta kokarin kunna laptop, don ymantar da ita. Yce, kinsan menene wannan? Ta a'a yace computer ce, agurin aikinmu aka rba mna. Ummi tace, kyauta? Yce A'a za'aringa cirewa acikin albashinmu, mtso kigani. Tdan mtsa inda zta iya kallowa, ykunna yna nuna mta abubuwa, yce ai nsan ki zaki iya sarrafata, tce wai, bazan iya ba Yaya Abba. Yce, nima sai nshiga mkarnta akwai tnan cikin gri zan shiga nyi diploma, salis shi tuni yyi. Ummi tce amma gshi ynzun mkana sarrafata, yce ina dan hwa ta office dinmu ai tce tayi kyau Allah ysa albarka yce amin. Ykashe komai ydauki take away din ynaci. Sannan yce, bri infita. Tdube shi itakam bta son yfita don umma tce mta tzama mai tsare mijinta dga zaman majalisa koyawo. Indai ba mkarnta yke zuwa ba, yma ztayi thana shi fita tatambayi knta, tdube shi cikin tausasa murya. Ya Abba hka zka fito bkayi wnka ba? Tmike gruwa nan nadiba bari inkai mka, shima ymike. Sai anjima zanyi ummi, ynzun shago nke sn zuwa. Akwai wsu dinkuna da za a amsa yau ina son ingako yaran sun gama snnan inson in yanka wsu dunkunan ciki har dnaki, koda yke saina gwada ma tukunna. Tce, tokadan huta mana ynzun faka dawo, ygane bta son yfita ne, don hk yce kda kidamu dg shago ba inda zanje. Har bkin kofa tarako shi tarike labule, to sai kdawo, yce to, ynzun mbai kalli inda

bishira tke ba, yyi wje. Datsaki traka shi tre dcewa, girma dai yfadi warwas, murmushi yyi mai sauti yfice abinshi. Ita kuwa sai thau zntuka, kinibibi a auran mka miji sannan a nuna anfi ka sonshi, yrinya lokaci nabaki. Ummi dai sai tkaro kofarta, koda dre abinci daidai cikinta bishira tyi taci tba 'yarta shiko Abba bai shigo gidan basai bayan sallar isha'i. Byan yje sun sha dirama da umma, tce itafa bta yi abinci dsuba, yce umma gskiya toki bmu na babanmu. Tyi driya, kasan abin dakake fada kuwa abba? Inbaku abincin mijina? Ai kuwa bkwaci ba. Tsohuwa tace, kai ina mtarka ita bazata dafa fa? Kodon tsoronta fakakeji ko? Abba yce eh bazata dafa ba ina ruwanki ke tsohuwa kin cika sa ido. Tce, nasa din, ai gskiyane kowa ysn uwargida ke yin girki harsati guda. Abba yce, to mu tsarinmu bhka bne, tkwashe da driya. Bwani tsarinku bhaka bne kila ma kinyin girkin tyi, yce oho dai bza kiji bdai, tce jeka intayi tsami mji. Umma dke tsheka driya tce, abbana zoka dauka gashi nan yce, yauwa ummana mungode, tce abba bka shiga gidan nanne? Yce wai gurin umman bashir? Tce eh, yce ina zuwa mna, tce todon Allah kadinga shiga, nan yyi musu sallama ytafi. Lokacin dya shigo gidan dindim! Sai daya tda injin, aranshi cewa yake yi lallai mta dakíshi, jimatar dko darana tada inji tke yi amma ynzun don kda wtan tga hske ko tji iskar fanka shine taki tadawa.I novels / ZURFIN CIKI book 4 part 7
ZURFIN CIKI book 4 part 7
Posted by Bashir Sani Fesan on 15 Dec 2016 - 01:41
Ya aje kular kofar dakin ummi yaleka dakin bishira, tana kwance kan gado, itafa bata jin cewa zata dazama dakishiya, dole cikin biyu ayi daya, kota tada ballin dazai saketa komuma tanemi duk wata hanyar daza akori wannan 'yar iskar yarinyar. Yashiga dakin, muhibba daketa wasa akan gadon da baya zaton tun da aka kafashi tasake kakkabe shi, yace hibba. Yarinyar ta waiwayo cikin murna tanufo ubanta da dan gwaranci, bishira tasa hannu tasuri 'yarta yace, bishira duk wannan abin daki keyi fabashine mafita agare kiba. Ki kwantar da hankalinki ki

nutsu ki kama girmanki, yarinyar nan zata biki amma in kin zabi akasin haka kece zaki koko.... Kai malam! Ta katse shi, bafa wata sauran magana fanasan komai, ni yanzun saki kurum nafi muradi, ya ce sakin lafiya? Ni yanzun ma na soma sonki, tadaga mishi hannu tare da daga murya, nikuma nadaina sonka, karya ne makace kana sona kuma kanason waccan banzar. Dole acikinmu akwai wadda kafi so. Abba yace to ai kece, ke nafi son kuma ita tasan haka, kalmar tashi tadan sanyaya mata zuciya. Don haka bata sake magana ba, yace kina bukatar wani abu ne? Tace don Allah nidai ka fita kawai, yace to na fita. Ummi lokacin tana canza kaya zuwa riga dazani na leshi, sosai tayi kwalliya tamkar kasureta ka ruga don kyau. Fuskarta sake ta tari Abbanta dasannu dazuwa, ita ce tasa musu abinci kowa da plate dinshi, amma sai ya aje nashi yace suci nata. Dama taso yin hakan amma tana tsoron kada ya gwasaleta, sai da sukayi dam sannan yace bari yayi wanka tatashi takai masa ruwan wanka tadawo. Kafin ya fito ta sake gyara ko ina, jallabiya mai gajeran hannu yasaka mara nauyi ya wadata jikinshi da turaruka tana kallonshi cikin sha'awa. Taso taimaka mishi tun agurin shafa mai, amma tana tsoron kada yaga zakewarta, don haka tashare tare da cewa dasannu za azo gurin. Ysake cewa zai koma shago, tace haba yaya Abba yanzun kuma? Yadauko tape dinshi nagwada mutane, zo in gwadaki, har da kayanki zan yaka yanzun. Yarannan 'yan shiriritane, badon naje dazun ba dasun sani nasaba alkawari, dinkunan su kawai suka yi tayi suka aje wanda nabasu. Ummi tabata fuska, ya tausasa murya, come on zo in gwada ki, bazan jima bakinji ko? Tatashi taje gabanshi ta tsaya. Sai dai mamakinta duk dunkunan da Ya Abba ya sha yi mata abaya bai taba gwadata basai yanzun? Koya manta yanda yake mata ne? Tsawon siket din ta ya soma gwadawa, tana tunani sai taji ratsawar dan yatsansa tare da tape din a kwankwasonta, duk da cewa dariga ajikinta saida hakan yasa taji

wani yanayi ajikinta. Har ma takalle shi, haka nan ya auna hips dinta da kirjinta, shi kanshi ya shiga wani yanayi alokacin, haka nan yakoma shagon cike dakewarta. Kayan bacci tasaka ta kwanta a gadon tana da yakinin bazai mata komai ba, tunda yasan bata sallah. Har kusan goma da rabi tana jiran shigo warshi shiru, waya tadauka ta rubuta mishi sako da cewa. Ya abba don Allah kadawo ni dai tsoro nake ji. Ya karanta yayi murmushi, azuciyarshi yace, don ita ya kwafe, yayi dunkunan yana son kudin don ya sai mata akwati da kayan shafa zuwa kayan ciki. Share ta yayi sai kusan sha daya darabi sannan yatashi tare da sallamar yaran, haka nan itama sai daya hado mata duguwa rigarta ta shadda wadda dama anriga anyi sirfani ajikinta. Dakin bishira yasoma lekawa, bacci yadauketa sosai agefen gadon take da alamun baccin yazo mata ba cikin shiri ba. Abba yayi murmushi tare da cewa, wa ya fada miki ana cin bashin bacci? Ina zaton matar nan jiya bata runtsa ba, yau gashi yazo ba shiri. Har ya gyara mata kwanciya itama 'yar ya gyara ta amma bishira bata farka ba, don haka yakashe mata wuta yafita. Yaso kashe injin amma garin da zafi gashi basu kawo wutar nepa ba, gidan yarufe yazo ya tura kofar ummi data rufe. Karar kofar ne ya farkar da ita amma bata motsa ba, tun daga kofar yatsaya yana kallonta, can tsakiyar gadon takwanta bata dora kanta saman filo ba. Amma tana manne da filo daya akirjinta fuskarta yake kallo, a jikinta taji kallonta yakeyi. Kusan minti 4 sannan ya aje ledar hannunshi. Shirin bacci yake amma yakasa daina kollonta, shikanshi yana mamakin wannar jarababben son dayake ma ummi, duk da dakewar dayake don kada yabada kanshi amma sai yadinga jin wani abu yana fisgarshi. Tamkar yafito mata da zallan sonshi gareta, tsoronshi inta gano kila tarainashi. Kadan-kadan takan bude ido ta saci kallonshi, sai daya gama komai a tunanin ta ya kwanta a gadon amma sai taga yadauki filo yakwanta a kan kujera. Haka suka rayu har tsawon sati daya, ranar yabar dakin ummi ranar kuma tasoma salla,

ita ko bishira satin nan tayi shine tamkar mahaukaciya sabon kamu. Ranar kuma da abba yadawo dakinta bata runtsa ba shima bata barshi ya runtsa ba, daga bisani dole yabar dakin yakoma falonta yakwanta. Haka gidan yaci gaba da kasancewa, in Abba yafita ummi bata da sauran sakewa saboda zagi da habaicin bishira. Wani sa'in har da kawayenta, ko makota 'yan jam'iyarta su shigo suyi tayi, ummi bata kula su.qnovels / ZURFIN CIKI book 4 part 8
ZURFIN CIKI book 4 part 8
Posted by Bashir Sani Fesan on 15 Dec 2016 - 01:50
Duk abinda bishira zatayi kada takulata. To ita duk bawannan bne damuwarta ba, damuwarta ynda Abba sam yaki nuna sha'awarta gare shi, duk dayasan tana sallah, hka nan duk lokacin dakwananshi yajuyo kanta sai dai ya jefa filo akan kujera ya kwanta. Takasa gane ma'anar hakan, tun tanajin dadin ynda bai nemeta ba saboda tsoronsa da take harta dawo tasoma jin haushi. Ita ma fa mutum ce cikakka mai lafiya, sannan tana kwana daki daya da san kacecen abun sonta ya ya ba zata damu ba? Sai dai tayi wa kanta alkawarin a yau in zasu shekara ahaka ba za ta taba yi masa tallar kanta ba ma'ana baza takai masa kanta ba. Sai dai zatayi masa kyale- kyale taga karshen girman kai, ta kosa su hadu da fati don ta bata sakon kananan kaya tasiyo mata don ta bata labarin cewa ta kwashe su a wambai. Kwananta goma taso ma girka, duk tsawon kwanakin nan abincin siyarwa dana umma suke ci, domin bishira taki dafa abinci. Ranar da zata fara girki ta haukata gidan da kamshi, tuwon shinkafa miyar shuwaka, tasan Abba nason tuwon shinkafa. Tun kafin ya dawo yamata waya ta aika shagonshi, 'yan shago sun ci suna santi, haka nan ya gayyaci abokansa kofar gida ya shimfida musu tabarma suka ci tare da lemu, zobo da kunun aya. (reall ehem tazubo mun nawa na koma 1 site ina kimtsa cikina lolx) ga nama ya wadata a ciki, abba yaji dadin yanda abokanshi sukayi ta santi, safiyar ranar kuma kunun gyada ta musu da kosai. Duk wannan abincin da ummi keyi bishira ko a harshenta ta ki

ci, cewa ma tayi ita fa kowa tayi girkinta don baza ta ci abincin ummi ba. Kuma ba shegiyar dazatai wa girki, hakan yayi wa ummi dadi don nata ganin ta bakin tsohuwa ce, da ta ce ko kwai bishira tadafa shine dai dai a cikin bawo to baza ta iya ci ba bare wani abinci. Sun zauna tsawon wata daya ahaka ummi bata taba leka ko kofar gida ba, tana kewar ummanta gara ma tsohuwa duk ranar juma'a in tadawo masallaci takan biyo gidan taga takwararta. Dakinta Abba yake yagama karyawa ya shirya zai tafi aiki, ummi ta kalle shi tana son tambayar zuwa gidan umma tna jin tsoro. Ya dubeta kamar kina son cewa wani abu ko? Ta ce am dama inaso inje gida in gaida su umma, yajuyo yadubeta suka hada ido. Gabanta yafadi, ta sunkuyar dakanta, yace a'a tadaga ido takalle shi, wani kunci taji aranta, ga matanshi nan yini take garari a layi bata ko tambaya amma ita ta tambaya shine ma zai hanata? Ya dauki jakar shi, ta mike ta rakashi har tsaka gida tare da yi masa addu'ar Allah yatsare, yini tayi da takaici dama haka mata suke ji in an hana su zuwa anguwa? Daran ranar zai koma ga bishira don haka bata san dawowarshi, tana kwance kan doguwar kujera tana karanta littafin hausa ( naleka muku kozanga sunan littafin amma bangano mukuba) kamshin turaren shi ne yasa tasan yashigo, don littafin yadauki hankalinta. Ta amsa sallamar daya sake yi tare da mikewa zaune, yana sanye da kananan kaya tamkar wani dan saurayi, yayi kyau a idonta kamar ta rungumeshi. Tace sannu dazuwa yace yawwa, dauko mayafinki muje tazura takalma bayan tagoge sannan ta ciro mayafi, yace a'a dauko hijabin. Ta maida ta dauko hijabi tafito sannan yakulle kofar, saida suka fita waje sannan yadubeta, hannu rabbana zakije musu? Tace yaya Abba toni bani da kudi ai. Sukabi ta wani super market suka sai sabulai da turare, akafa suke takawa sannu ahankali suka jero duk da cewa bawata hira suke ba, Abba ne yake amsa waya jifa-jifa na jama'a masu sonshi. Tun daga nesa suka hangi mahaifansu suna cin abinci a inda

suka saba. Alhaji babba dakarami. Cikin zumudi ummi ta ce, yauwa gasu alh. Abba yaje haka zakije musu da rawar kanki ko? Cikin shagwaba tace, wanne rawar kai nayi toni yaya Abba? Yace, na gani kinayi kamar zaki kwasa da gudu, kafin tayi magana sun iso gurin dukkansu suka zube akan tabarmar daga gefe. Abba ne yasoma cewa, sannunku alh. Alh. Yace, a'a kune? Alh karami yace, uwata harda ke? Tace, eh ina yininku? Sukace lpy lau. Alh. Karami yace, uwata kunanan lpy ba wta matsala ko? Ta ce, ba komai alh.. Yace to Allah yyi maku albarka, ya azurtaku da 'ya'ya ma su albarka wadanda kuma zasu biku. Abba yace amin suka hada baki da Alhaji babba, alh babba yaci gaba da cewa, Abba ya hakurin shirmen ummi kuma? Ince dai bawata matsala? Abba yakalleta mun gode Allah alh, amma bwata matsala, ummi tamike dazumudi bari a karasa. Tun daga soro take kwala ma umma kira. Umma tce, A'a muryar wa nake ji haka? Ummi tashigo da gudu ta cakume umma, tsohuwa tafito tana fadin lale. Dakin tsohuwa tasoma shiga suka gaisa sannan tadawo dakin umma, sun gaisa umma tasake mata nasiha, ummi tace umma ni matsalata daya matarsa. Kullum saitayi min habaici tana zagina wata rana r harda kawayentaRFIN CIKI novels / ZURFIN CIKI book 4 part 9 ZURFIN CIKI book 4 part 9 Posted by Bashir Sani Fesan on 15 Dec 2016 - 01:54 Ita ko bishira gidan su umman bashir ta tafi dakuka wiwi, tace Abba yamata duka takan sun taka hakkinta sun fita ranar girkinta. Tayi magana ummi ta mata tsaki shi kuma yazo yazo yahauta da duka, umman bashir tace duka! Duka akan ummi? Tabdi, tashi muje gurin wadanda suka daure masu gindi. Umma na kokarin shiga daukin alhaji taji sallamarsu sama-sama, gabanta yafadi ta amsa tare da dawowa baya. Sahura tace to suwaiba, abinda kuka shiirya yasoma tasiri. Abba yayi wa bishira shegen duka saboda 'yarku, umma tace haba sahura, yaya ki ke irin wannan maganar? Mu ne zamu sa Abba ya cutar da iyalinsa? Sahura kiyi nazari. Alhaji yafito, me yafaru ne ni kejin hayaniya suwaiba? Umma tace, oho. Sahura tace, bishira fada musu. Nan bishira ta shaida masu yanda ta tsara ma umman bashir, alhaji yadaga waya yakira Abba, Abba yana dagawa alhaji cikin zafi yace Abba maza kazo yanzun duk in da kake. Abba yace to alhaji, ummi ta mike zan bika tsoro nake ji ni daya, cikin zafin rai yace abin daki ke tsoro ya cinye ki, ya fita fuuu. Cirko-cirko ya same su a tsakar gida, sai muryar sahura kake ji tana rashin mutunci. Alhaji karami yadawo gidan shi sai ya jiyo muryar sahura a can gidan, ya nufi gidan don haka kusan tare suka shiga gidan da Abba. Alhaji cikin bacin rai yafada Abba da fada, abba bai katse shi ba har sai daya kai ga tambayarshi cewa me yasa yayi mata duka? Yace, banyi mata duka ba alhaji marinta kawai nayi, umma ta ce mari kawai ne Abba? Alhaji karami yace, to kan wane

dalili ma zaka mare ta? Abba ya koro musu komai, ya kara da cewa, wannan har zata ce an mata tsaki, zata yi duka ni wane irin zagi ne bata min ina hakura darajar iyayenta? Ya nuna ta, wallahi in kika kai ni bango zaki koma gidanku don bazan iya ba na gaji, nan kuma su alhaji suka shiga bashi hakuri. Ita kuma suka bata rashin gaskiya, sai dai duk da haka umma tai masa fadan kada ya sake daukan ummi ranar girkin bishira ya fita da ita, yace to. Umman bashir taja bishira zo muje ai dama nasan baza suga laifin 'yar su ba. To wllh marin da yamiki ki tabbata bashine. Ko nan da yaushe ne ki rama shi kan ummin, in ba haka ba duk da banice uwar data haife kiba sai na tsine miki. Alhaji karami yace, to katuwa mara lissafi, ke dai kinji haushin rayuwarki, to ki sani duk randa ta rama duka akan ummi ni kuma akan ki zan rama wa ummin inga ta tsiya. Alhaji babba yace, kada kai ma kazama su mana aminu. Tsohuwa tace, gskiya ne, in har tazama silar dukan ummi itama sai ya mata taji. Umma tace, a'a duk abin ba zai kai haka ba insha Allahu, kai dai abba kayi ta hakuri sannan kadaina sa hannu kana dukan mace. Yace, umma dukana fa tayi, sai kace wani soko zan tsaya mce tna dukana, umma tace, to ai tace ummi taje duka, yace ummin 'yarta ce? Alhaji yace, tafi gidan kahadasu kayi masu nasiha, Abba yace ai baza ta tsaya ba, wannan yarinyar fa sai dai addu'a ni in nagaji kawai hakura za ayi, umma tace bana son jin wannan zancan, alhaji karami yace ai gskiyarshi ne, shi yasan irin zaman dayake da ita. Alhaji babba yace, ai kuma darajar mahaifinta za aduba, da mutuncinsa, Abba yace ai dama alhaji ni banda mahaifinta da tuni nayar da kwallon mangwaro na huta da kuda. Umman tace je ka gida Allah ya kyauta. Nan dai ya musu sallama yanufi gida. Ummi da gske tsoro ne da ita, da rana in ba kowa bta damuwa, amma da dare tfi son tdinga jiyo motsin bishira koda habaicin dta sabayi mata. Soro taje ta tsaya tana yi tana leka waje, can ta hango bishira, don haka takoma daki ta kullo kofa aranta ta ce kada tazo tayi min duka. Ummi tna jiyota lokacin data shigo tana cewa wllh kan yarinya zan rama marina, wannan dole ne koba dade saina ramashi. Abba kan bai nufo gida ba, shagonsa ya wuce lokacin goma ta gota, yaran sunyi shirin tafiya, don haka ya amshi makullin ya shiga shagon saman teburin da suke yin yanka da guga ya hau ya zauna. Tagumi ya zuba hummu biyu tare da sauke wata ajiyar zuciya mai karfi, me yasa ummi ta furta kalmar data tuna mishi cewa bata sonshi? Sakankancewa dayanda ummin kenuna mishi yasa shi jin kamar sonsa take ashe dai shi yake shermenshi. Ya tuno wani labari yaya tabaji na wani mutum da aka ara masa mata wadda bata sonsa, tazo tazauna dashi tsawon shekaru kuma tayi masa biyayya matuka. Ga 'ya'ya sun haifa yaran sun yi girma sosai, suma sun zama magidanta, sai wata rana mutumin nan suna hira da matar, yace oh, wance dafa ba kya sona, yanzun gashi harmun tsufa kin manta dawata kiyayyah. Tadubeshi, inji wa yace maka na manta? Biyayya kurum nake maka amma har gobe bana sonka. Abba yajinjina kai, lallai dole ne ya nutso, yadaina tunanin ummi tana sonshi kokuma zata soshi, shidai da kaddarar sonta tafada mishi sai yayi ta addu'a Allah ya bashi hakurin jure zama da ita ahaka. Bai san adadin lokacin daya dauka awaje ba kuma baisan adadin tunanin dayayi ba. Daga karshe yarufe shagon yanufi gida. Ganin yanda garin yayi tsit shine yasa shi kallon agogon hannunshi, daya da minti shabakwai, lallai lokaci yatafi. ZURFIN CIKI book 4 part 10

ZURFIN CIKI book 4 part 10

Posted by Bashir Sani Fesan on 15 Dec 2016 - 01:55

Yanufi dakin bishira aranshi yce da wanda yake
kinka gara mai sonka ko mahaukaci ne. Gdon

yahau tagefe ya kwanta suka saka muhibba atsakiya, ummi kuwa duk tsawon lokacin nan tkasa bacci domin bata ga shigowarshi ba. Idonta biyu har sai daya shigo ta leka ta windo tana kalloshi har yashiga dakin bishira ya rufo kofa, sannan ta kwanta tare dayin ajiyar zuciya. A fili tace ina ga fa har dani alaifin nan, amma bari gari yawaye inba shi hakuri durkusa ma wada ai ba gajiyawa bane. Bishira tafarka cikin dare taga Abba kwance hannunsa na dama dore kan jikin 'yarsu, ta tsura mishi idanu tana son mijinta sosai. Ban dahaka data kaishi koto ya bata takardarta koda mahaifinta xaimata baki sanadiyar haka, amma shi yanzun yadaina sonta. Takai hannu tadora a kumatunshi, ahankali yabude idanu, suka kura majuna ido yace bishira me yasa kike yin abinda zai samu mu samu sabani bayan kinsan sone ya hadamu? Idanuwanta suka kawo ruwa, Abba dane ka soni kaji dani har alokacin ina ganin ba Wata mace data kai ni dacen gwanin iya soyayya. Amma yanzun duk ka zuba ni a kwandon shara har kana marina saboda ummi. Ya ce, a'a ba sbd ummi na mare kiba, saboda kin dukeni ne amma kiyi hakuri. Banason kina zubar da kanki a gurinta, yawan fadanku zai sa raini ya shiga tsakaninku, ni kuma ba zan so ta rainaki ba. Kuma da kin kwantar da hankalin ki ummi fa ba wai tana sona bane, ita fa an matsa ma tane, kuma su umma da kike zagi na rantse miki masoyan kine. Ta ce tokai kana son ummi ne ? Ya dan yi jim, sannan ya ce ai dai kin san yanda auran namu da ita yakasance bagatatan bai dace ace kinma tsaya yin wannan tambayar ma. Tadan yi shiru, zancen nan ya shige ta bakamar yanda ta zata da farko ba, ko dadin baki zaimata? Sannan ta tuno da ranar da fati tazo. Ta labe taji koza suyi zancenta sai taji suna ta hirarsu, acikin harar fati ke cewa wai kuwa ya kuka kaya ne ummi? Nasan yanzun ai kin warke, kema kin goge. Ta ce damefa? Fati tace, a'a ki gane mana, batun kwanciya. Ummi tace, kin san cewa yaya Abba ko gadona bai taba kwana ba? Fati tace kai haba?

Ummi tadinga yimata rantsuwa, tuno da wannan sai bishira ta yarda mijinta ma baya son ummi, don haka sai ta saki murmushi. Yace, tunanin me ki ke yi? Tace da ina ga kamar dadin baki kake min, amma dana tuno naji ummi tana fadama fati wai baka taba ko kwanciya a gadonta ba, bare ka hada jiki da ita sai na yarda. Abba ya zaro ido, a ina kika ji suna zancan? Ta ce, a'a tazo mata rakiyane naji suna maganar a soro. Abba ya girgiza kai. Bishira tace, kuma da gske hakane, yakai hannu yakama nata tafin hannun, wannan wani sirri ne tsakanina da ummin. Ynda ba zan fada mata komai tsakanina dake ba, haka itama zan sakaya nata sirrin, tadai fahimci hakane, don haka sai ranta yayi mata dadi har ma ta baiwa Abban kanta a daran. Ynda taga yna rawar jiki ya tabbatar ma ta ba wani angwanci da yayi, don haka zuciyarta fes ta wayi gari. Duk da cewa abba ya tashe ta cewa taje tayi wanka harda Allah yahadata amma tayi niyar baza tayi hakan ba sai gari yayi haske. Ummi ta fito don tanuna mata cewa Abba ya kwana da ita. Bishira an dafa ruwan tea an kai falo sai wannan rawan kai ake yi. Sai data lura ummi ta dauko tsintsiya tasoma sharar gidan kamar yanda tasaba, sannan tafito da buta aka nufi bandaki, kai ko dankwali babu aka yiwanka aka fito. Gashi yna ta digar ruwa, ummi ta fahimta kuma tagane cewa tayi hakan don ta nuna mata ne. Kuma taji zafi aranta kamar ynda bishiran taso, ta amma azuciyar ta sai tace na banza jiya nan yakora miki mari. Lokacin da abba ya shigo gidan tagama shara tana kwashewa, bai ko dubeta baya shige falon bishira, kan ummi yasake daurewa, me yake faruwane haka da zafi? Ta tambayi kanta. Data koma daki tagumi ta zabga tana tunani ita da suka yi kaca-kaca ma sun shirya bare ni? Kamar tabi shi har falon bishiran ta gaida shi, amma sai tafasa. Tazuba ido taga zai bar gidanne ba tare daya leko dakinta ba? Sun gama karin kumallonsu tsaf yayo wanka don tafiya gurin aiki, sai dai kayan dazai saka suna dakin ummi. Ya fito yanufi dakin. Ciki- ciki yayi sallama ita kam

tsoro ne ya tsirga mata, tasake tambayar kanta mekuma yafaru? Ta amsa tare da gaida shi. Nan ma a ciki ya amsa, yadauki kayan sai dazai fita sannan yace ba kya bukatar komai ko? Tayi karfin halin cewa sugata ceta kare. Ya dube ta furka tsuke me yasa baki fada minba? Ta ce, na manta ne, yace to sai kije gurin bishira da dibar miki inzan dawo na siyo. Ba kya neman komai da rana ko? Tace a'a sai nama kawai ya daga murya, kullum ne ya zama dole a saka nama a abinci? Jikinta har bari yake don tsoro, ta ce a'a yaja tsaki ya fita. Ummi tasaka kanta cikin cinya tana furta 'inna lillahi wa inna ilaihir raji'un.' hawaye suka soma yi mata sintiri.KI novels / ZURFIN CIKI book 4 part 11

ZURFIN CIKI book 4 part 11

Posted by Bashir Sani Fesan on 15 Dec 2016 - 01:57

Dadi tamkar yakashe bishira don tna labe tana jinsu afalon ya saka kya yashirya tsaf, sannan ya nufo dakinta don dauka jakar laptop dinshi. Jin sallamarshi tayi mza tashare hawaye sannan ta amsa, yshigo ya dauko dari biyu ya aje mata akan gdo, ga kudin maman nan kura, kada fati tzo kifada mata baki kudin nama kullum tunda har kin iya shaida mta cewa ban tba kwana agadonkiba. Kin kosa inkwanta dakene? Yadauki jakar yarataya sannan yayi mata wani kallo sama dakasa, to banga gurin kwana agadon naki ba. Hakanan banga abin kwanciya ajikinki ba, yafice yabar ummi tsaye tazaro idanunta cikin matukar al'ajabi da kunya. Ina ya Abba yaji zancen nan? Kodai fati ceta fada masa? Wata zuciyar tace fati baza ta iyayi masa zancan nanba saidai in ummarsu tafada mawa ita kuma tafada masa. Inko hakane fati batayi mata adalci ba, ai hira ce irinta aminta tsakaninsu, gashi ta bata kunya har tasa ya Abba naganin tazaku. Tokuwa tasha alwashin nuna mishi bahaka take nufi ba, afili tace Allah yabamu rai da lpy. Sai kuma tasoma kuka. Bishira tafadi kan dadi ashe gara data fada masa zancen dataji suna yida fati, gashi yanzun yayi mata rana. Lallai labe yayi mata amfani sai kawai tasabi 'yarta tazari mayafi tafice makota, yau kan tana da labari mai dadi sai yawon raba

shi take bata manta ko kalma daya. Sannan darana tazo tahau kici-kicin dora girki, lokacin ummi tafito don yin alwala, ita ko karyawa batayi ba don tawuni da takaici ya Abba. Tana kallon yanda bishira tazubu kayan miya tana jajjagawa batare data wanke ba hancin kawai ta cire. Ummi tayi alwala tashige daki, ranar har dare ummi bataci komai ba, duk da tanajin yunwa. Zantukan abba kawai kemata yawo a kwanya. Tayi kuka harta gaji fuska ta kumbura. Tun uku yadawo baiga ummi ba, bishira tagabatar masa da abinci dakyar yayi cokali uku. Dama yazo dafura, yasha sannan yanufi shago, yini yayi yana tunanin kamar bai kyauta ma ummi ba, amma yana mamakin yanda ummi ta iya cewa bai hau gadonta ba. Kenan inyahau din dakuma abinda yabiyo bayan hawa gadon duk zata ringa fesarwa ne? Kai yafaji haushin abu biyun nan dacewa bada sonta aka daura masu auran suba dakuma fada ma fati sirrinsu. Saidai duk dahaka zuciya da idanunshi suna matukar kewar ganin ummi, sai shida yadawo gidan. Ruwan wanka ya diba yanufi bandaki, man shafawarshi dasauran su suna dakin ummi, don haka yakalli bishira. Bari in dauko kayana can dakin ummi kozaki dauko min? Tace, bazan jeba kaje da kanka. Tana kwance kan doguwar kujera lokacin kanta yana matukar sarawa, don kuwa yanda yayi sallamar da kyar itama dinda kyar ta amsa. Saidai ita badon wulakanci tayiba, saidai don yanda take jin jikinta. Yashafa mai tare da feshe jikinsa da turaruka. Idanunshi suka sauka kan darinshi biyu daya aje mata. Yakalleta, ke ina abincin da kika dafa? Batare data dubeshiba tace, bandafa ba. Yace sbd me? Tace banjin yunwa, kaikuma naga ba anan kake ba, baki ya taba yasa kaya yafice. Har tayi sallar isha'i lokacin tasoma jin jiri, amma bata da niyar shan ko tea tanajin ya shigo ya aje mata ledar ta kusan minta 30 kafin tataso tazo tatura kofarta. Sannan taduba ledar, nama ne balango yaji albasa da tumatiri, sai sugar da madara, nan ta aje su tayi kwanciyarta afili tace natabbata kurar kenan indai naci maman nan.

Bacci yadauketa can kusan ukun dare fa yunwa fatakai yunwa, kowa yasan yunwar dare yanda take jigata bawa, a gigice ummi ta tashi tahada tea tahau sha da gaggawa. Tagama kamar taci naman sai kuma tafasa ( tamiko min ninkuma nayi fuska nacinye au namanta madawani azumi lolx) ta kauda kayan ta koma ta kwanta, aikonan fa cikinta yahau hautsinawa. Dagudu tatashi tanufi fita tana bude kofa kafin takai bandaki tasoma sheka amai, tun bude kofarta abba yafarka dasauri yafito. Riketa yayi ganin yanda take sheka amai kamar zata amayar da hanjin cikinta, sai sannu yake mata. Data gama yajanyo ruwa ya wanke mata fuska ta kuskure baki. Yawanke gurin gurin tana gefe tsugunne, cikinta da kanta sai ciwo sukeyi tana mikewa sai jiri. Nan tafadi ragwaf, shine yadauketa tamkar ya dau jaririya don rashin nauyi yace duk kece kikayi makanki sanadin wannan matsalar. Don kina fushi saiki yiwa abinci yaji, ai gashi nan kema kina ji ajikinki, kan kujer yadorata ya cire mata siket din atamfar dake jikinta, don duk sun jike sai na ciki. Yajuyata zai zage mata zif din rigar tana son ta hana amma bata dawani karfin hanawa. Tanaji tana gani abba yacire mata riga, gashi ko best bata saka ba sai breziya. Takai hannuwanta tarufe kirjinta. Shikam ganinta ahaka yasa tsigar jikinsa tashi, tun daga karamin yatsansa har tsakiyan kansa ruf da ciki ta juya tayi, shi kuma ya kunna mata fanka yafita. Zaune ya samu bishira atsakiyar gado, ta kalle shi da tuhuma, me kaje yi dakinta? Yce amai naji tanayi shiyasa nafita, bta dlpy ne, tsaki taja sannan ta kwanta. Shi kam bai runtsa ba, kunnanshi da hankalinshi suna can, dga bisani madayaga baccin yaki sai yatashi yayi alwala yasomayin nafila. Dazai tafi masallaci yske lekawa yaga IKI novels / ZURFIN CIKI book 4 part 13

ZURFIN CIKI book 4 part 13

Posted by Bashir Sani Fesan on 15 Dec 2016 - 02:05

shikenan yanyun bata dawani aji agurin Abba ummi da tsoron allura sam taqi tsayawa jiya ma don agalabaice take Nurse din tace ke dai shagwaba ta miki yawa A ce allura ma kin kasa

tsayawa kefa mace ce Wata rana ma haihuwa zakiyi ummi fa taki tsayawa nurse tazo tace ma Abba taki tsayawa abba yaleka dakin allura menene haka ummi tsoron alluran ki yayi yawa kitsaya mana Tadube shi fuska a shagwabe ya Abba dazafi nikam na hakura da allurar nan Abba ya shiga dakin ya kalli nurse din zo kimata ba zanyi asarar kudina ba Ummi bata ankara basai jinta tayi atsakiyar kirjin Abba shi kanshi sai jin wani abu yayi yataso daga tafin kafarshi zuwa tsakiyar kanshi Har yayi baya dasu tamkar zasu fadi to bare ummi wadda jikin nata ya dauki rawa Ya kalli nurse dinda idanuwanshi wadanda suka canza kala nan da nan zo kiyi mata Yadaga hajabinta tare dazame zanin daidai inda za ayi mata allurar shigar allurar ta saka ummi cewa wash tare da sake makalewa jikin Abba Don kuka tasaka wanda daga jinshi kasan shagwaba ce zalla ya lumshe ido lokaci daya ya kuma budesu nurse din tace kai ke kam kin cika shagwaba Abba ya dora yatsunshi guda adaidai gurin da akayi allurar yana murza mata tare da rada mata 'sannu' akunnenta Rekicewa tayi sannan ta kwace jikinta daga gare shi wani yanayi ta tsinci kanta mai girgiza bawa Ya sauke ajiyar zuciya sannan yace mu tafi suna cikin mota dukkansu sunyi shiru Abba kasala ce da muradin matar shi yasa shizama hakan Ita ko ummi mamakinta ba yau Abba yasoma taba jikinta ba can baya yasha rike ta yazane ta, yasha rungumeta ayi mata allura, bata taba jin irin abinda taji yanzun ba Ta jingina da kujera tare da lumshe ido sai take ta tuno yanayin dataji lokacin daya mannata ajikinshi. Tsayawar motar ne ya sata bude idanunta, azatonta gida suka zo,sai taga ashe gurin kayan kwalama ne Ya kalleta, ina zuwa Ya fita ya nufi zuwa ciki jim kadan ya fito da ledoji, kaji ya siyo da madara mai tsafta, har da kankarar dayaji tana tambayar umma yasai musu. Tace, gama fa kankarar umma tasai mana. Bishira ta cika fam don takaici, kamal kaninsu Abba yaduba mata ko ummi tana gidan umma, ya fada mata bata nan. Ta tabbatar suna tare, ta

cema umman bashir tunfa safe suka fita tare umma tace tun safe wane iri? Tace wai bta da Ipy yaje kaita asibiti Umman bashir tace Allah ya tashe mu Ipy Goben nan zan tafi kauye dama gobe ta ce indawo gaje 'yar bori, ina fada miki ummi dakanta zata bar gidan basai ance mata ba. Bishira tace dahaka zata faru zanfi kowa farin ciki, umman bashir tace kece aida shegen kyamar 'yan kauye bakison mutane Matsalarki kenan da ace zaki jure muje tare kiyi kwana 2 'yar bori da bokan tsauni zasu cika miki aiki Bishira tace zanje umma. Biyan bukata ai yafi dogon buri umma tace taki turo minshi ince masa sha'ani zamu don kada yace zai hana, bishira tace to. Sun sameta agidan ummi tayi dakinta da ledar ta shikuma yashiga gurin bishira. Ranar daya dawo dakin ta kuwa tayi kyau cikin doguwar rigar shadda ruwan kunkumadi, tun yana kallon ummi asace harya kasa dauke idonsa Ummi talura ta birgeshi sosai don haka tazauna bakin gado tana fuskantarshi hira ce suke yi jifa- jifa itace ma tasoma sako zancen Ya Abba zance ma alhaji yasai min TV nagaji dazama shiru Abba yace a'a banason haka ina sane zansai miki, tace to Bishira dake labe ta girgiza kai aranta tace ashe za ayi bala'i duk randa yakawo TV ai itama ai iyayenta suka sai mata. Tace to yaya abba inason makaranta ya aje laptop din daya soma budewa yamaimaita kalmar makaranta? Ta ce eh, yace sai nayi tunani Ummi ta marairaice tunani ya Abba? Kai dakake son inyi karatu? Yace shikenan haka sukayi ta hira har lokacin kwanciya ummi tayi shafa'i da wuturi tayi shirin baccinta takwanta Abba yau yakasa nutsuwa tamkar yaje ga ummi, amma girman kai ya hanashi. Ranar sama-sama yayi bacci sau biyu yna fita yana watsa majikinshi ruwan sanyi kozai dan samu nutsuwa. Har lokacin daya tafi gurin aiki bashi da wani kuzari. Ranar fati tazo lokacin bishira ta tafi badadinta, ummi tahau fati damasifa tare da fada mata yanda sukayi da ya Abba. Fati ta rantse tamaya kan cewa ba wanda yasan zancen nan don bata fada ma kowa ba,

sukayi ta tunanin ta ina ne zancan nan yafita? Fati tace to ko kiyi hankali koda Anty bishira tana miki labe? Ummi tayi shiru tna nazari, can tadubi fati Bazan zargeta ba, domin ban taba ganinta ba amma zansa ido fati tace gara kisa kam yanzun harzuwa yau baku sasanta ba? Ummi tace aini bana bukatar sasantawa dashi tunda yace baiga gurin kwanciya agadona ba Fati tasaka dariya ke dai kada kicika baki,ummi tace kedai mu bar wannan zancen inbaki kudin kayan don Allah? Tati tace kibani dan bnida matsala mijina she ne yakaini nasai nawa zance yakaini insai miki kinason wanduna Ummi tace kinjiki da siket zaki debo min Ai har gajerun wanduna ki kwaso min, wulakanci zanyi a gidan nan.vels / ZURFIN CIKI book 4 part 15

ZURFIN CIKI book 4 part 15

Posted by Bashir Sani Fesan on 15 Dec 2016 - 02:12

Saidatayi sallah sannan tazauna gaban madubi duk da shirin bacci take yi Saida tashafa manta da hoda sannan tadan goga jan baki. Tafesa turarenta ta isa gurin kayan baccinta dake cikin dirowar dora akwati, ta dauko duguwa tazira sannan takama karshen kitsonta tahada su guri daya ta tufke. Zata ha gado yace, ga nama kizo muci. Ta fada gado tare da jan filo ta dora kanta da kirjinta sannan tace nama saikace wata kura? Dazun fana danci amiyar danayi. Yace nida na siyo shine nazama kuran ko? Tace, a'a ya Abba kaine ranar nan naji kace kura. Kullum ake cin nama? Yayi murmushi aranshi yace, ok nan na rama ne kenan, sannan yace toshi kenan bari in ajiye miki naki. Nan tayi kwanciyarta. To 'yar gidan tsohuwa, yafada danufin zolaya, tace kai kuma dan gidan ummanka. Cigaba yayi dashiga yanar gizonsa, ita kam a gajiye take bacci yasoma fizgarta. Lokacin dayazo shima ya kwanta akan gado, ta bude ido Ipy Yaya Abba? Ya dubeta tsakaninsu mutum daya zai iya kwanciya. Wace irin tambayace wannan mutum da dakin matarsa da gadonta atambaye shi Ipy? Tatashi zaune, gani nayi ba guri agadona, yayi shiru, wato ummi bata barin bashi, ta tsura mishi ido tana jira jin mezaice. Yatashi zaune, idanunshi

akan lebunanta, toni dai ga guri na samu, ta sulale itama takwanta rigingine tare dajan bargo tarufe rabin jikinta. Shima hakan yayi, ummi fargaba ce tasa tanemi bacci tarasa, shikam addu'ar bacci yakaranta sannan yashafa yalumshe idanu. Duk su biyun bacci sama- sama sukayi koda Abba baisamu nasarar kama kayan ummi ba amma aranshi yace wannan sharar fage ce. Dasannu za'a kai ga muradi, ko washegari daya kwana adakin dai bawani cigaba sai sake-sake Abban yayi tayi azuciyarshi, na cewa yakauda wata kunya ya fito mata amutum, amma yakasa hakan. Musamman yanda yaga ummin tana da shegen wayo, ba kamar yan yazata ba. Sannan gashi ta iya yin ado irin na tsokana. Hakan yasa duk ranakun girkinta Abba yana zumudi amma yakanyi kwanan rashin sukuni. Wata jumma'a tsohuwa ta riski ummi da irn wannan shiga tariga da gajeren wando, ta kawo mata ziyarar data saba inta dawo masallaci. Salati tasaka tare da cewa, yarinyar nan kece haka kinzamo sai kace arniya? Ummi ta tashi tsaye tayi juyi tare da cewa. Ynzun tsohuwa ban birge kiba? Ta ce kitson naki ne kurum yamin kyau, amma wannan shiga dame tai kama? Kuma shimai sunan malam yakasa hanaki koke ma yasoma tsoron nakine? Ummi ta tuntsure da dariya, ba tsorona yake jiba, shine ma yake son kayan don shine ma yasai minsu. Tsohuwa tace, oho! Eh lallai ta mike Allah ya taimaka, duk abin ku dai baza ki koma baturiya ba, ummi tace oho dai ke dai kuma baza ki iya wannan ba. Tace, Allah ya tsare nida wannan shiga, ummi ta dauko dari biyu ganin tsohuwa ta mike, nizan tafi in dan zazzaga in ziyarci jama'a. Ummi ta kama hannunta ta saka dari biyun, gana goron jumma'a, Allah ya hadamu aladan ziyarar. Suka fito tana cewa. Ke kullum nazo sai kin bani kudi ummi, to Allah ya shi muku albarka, Allah kuma yasa ki sauko lpy. Murmushi ummi tayi duk 'yan gidan su kallon mai cike suke mata. Duk hirar nan tasu bishira najinsu, ta cika tayi fam. Dama Abba yana kwana da ummi? Ashe shine yake sai

mata kananan kaya? Ashe har tana da ciki shine yamata karyar cewa baya sonta? Tana dawowa raka tsohuwa, bishira ta kalleta, karamar yarinya ta iya karuwanci, dube ki. Ummi ta kalleta babba fa ya rike girmanshi inba haka ba inhau in taka, kuma niba karuwa bace, kema kalle ki. Ta taso zan zane kifa? Ummi ma tadaga murya. Sai kace wata 'yarki? Ba ki isa ba. Bishira tazo zata shakota, ummi ta daka tsalle taja baya. Karki sake ki taba ni. Nan fa gidan ya kacame, bishira sai ashar take zugama ummi, tana kiranta 'yar matsiyata. Ummi tace, banga kamannin masu arziki ba a jikinki, nan makota suka shigo yin rabo. Ummi ko tana fada mata take ramawa, abin da yafi yiwa ummi ciwo datace ummanki matsafiya, nasan komai saboda bakin asirinta ne sahabi yafasa aurenki aka mannawa mijina. Don shima ya fada min ba ya sonki, har yanzun bai taba kwanciya dake ba. Ummi tace, kazama mara sallah me labe, kina labe min akofan don bakin kishi, kuma insha Allahu sai Allah yasakawa ummata tunda kika ce tana asiri. Maman amir kawar bishira tuni taruga takira umman bashir, sai dai cikin sa'a tanazuwa Abba nayin parking. Ganin yanda mahaifiyarshi tashiga gidan cikin hanzari haka shima agurguje yafada gidan, ranshi yayi mugun baci yanda yaga gidan cike da jama'a. Ga bishira mutum biyu sun rike ta tana zambarmar asake ta ta lallasa ummi, ga ita kuma ummi tsaye akofarta kanta babu ko dan kwali ta sha gajeren wando ya dan gota gwuiwarta da 'yar riga tana maida martani. Yace ma matan dasuka rike bishira, ku saketa suka sake ta ya daka mata tsawa da karfi, duk ku fice min daga gida, magulmata tunda duk yawanku kun kasa sasanta su. Sum-sum suka wucesuna tabe baki, duk dahaka bishira bata daina magana ba.ZURFIN CIKI book 4 part 16

## ZURFIN CIKI book 4 part 16

Posted by Bashir Sani Fesan on 15 Dec 2016 - 02:14

Haka umman bashar batasan yarda komai ya faru ba. Amman ta shiga zagi da tsine ma ummi har da ce mata karuwancin ne ya motsa, ai dama nasan tun kafin kixo gidan nan kinsan maza.

Bishira ta ce umma wllhi ga babban mai laifin nan, muna funtata sukeyi duk ire ire wadannan kayan na jikinta shiya sai mata su, ni bai siyo min ba. Na gaji da hakuri ana cutata gwara yaban takarda ta. Umma tace daina fadin ya baki takarda insha allahu saidai ita ya bata, Abba yayima bishira wani kallo tare da cewa ki tafi mana sai me? Yarda kika gaji da ni nima Haka na gaji da ke, ya kalli ummi yace ke kuma mi nake fada maki kullum? Itama cikin fushi tayi magana toh shikenan saita ta zagina tana ma ummata sheri don ita kake so? Bishira ta cafke dama ai ya fadaman baya sonki. Ummi ta kalleshi ko zai kare kanshi, amman baya kokarin Haka saima kara zaro mata ido da yayi yana cewa. Ni kike ma ihu ummi? Zuciya tazo mata wuya nata ganin an daketa ne kuma an hanata kuka. Shi kanshi ya tozarta ta da ya fadama kishiyarta baya sonta. Duk da tasan da haka ta kalli bishira cikin daga murya tace, an fada maki na damune don baya sona bana son ya soni don nima bana son Shi.... Mari Abba ya sakar ma ummi da bayan hannu, kalmar da ya tsana kenan, zafi yakeji a Zuciyarshi ko tunowa yayi da ummi bata sonshi. Daki ummi ta fada, ta fada kan gado tana kuka, ya kalli bishira kije gidan ku sai nazo, umman bashar tace ba inda zataje kuma in ka sake na samu labarin ta tafi saina debe maka albarka. Tasa kai fuuuu ta fice, tunda ka dauki hukunki mai kyau ka duki marar kunya ai naji dadi. Bishira ma taji dadin haka, Shi kuwa ba don su yayi ba zafin furta bata sonshi ne yasa ya daketa. Yana shiga dakin ummi lokacin ta mike tana kuka, ta dauko zane ta daura tana kuka sosai. Ta zari hijabi ta zura zata fita, yace ina zaki? Taki sauraronshi zata fita ya rikota, ina zaki nake? Tayi magana cikin daga murya cikin muryar kuka tace gidan ubana kai kuma ka zauna da warda kakeso, tunda ya mareta nan ya gane bai kyauta mata ba, don yasan ba dole bane ta fahimce Shi, sai ya samu kanshi da jawota ya rungume. Duk da suna cikin bacin rai Duk kansu saida sukaji wani irin yanayi. Yace kada kiyi yaji ummi kinsan dai koh

kinje su umma fada zasu maki. Cikin sanyin murya yayi maganar, kan ummi ya sara, ta kwace daga jikinshi ta sake fadawa kan gado. Sabon kuka ta saki, ya zauna bakin gado ya kamo hannunta ta sarke ya tsunshi da nata ya dan matsa, ummi! Ummi!! Tashi kiji, cikin kuka tace mi zanji yaya Abba, kawai ka rabu dani, ni baka man adalci ba. Ya za'a yi kaje kana fada mata ni baka sona kasa tana man gori, umman bashar harda ceman wai ni nabi maza. Ya sake kwantar da murya yace ki yarda ni ban fadama bishira cewa bana sonki ba, kuma batun umma kisashi a gefe kawai don ni nafi kowa sanin halinki. Nafi kowa sanin tarbiyar umma na... Duk da haka ai baka kare kanka ba lokacin da take fada ba, ummi ta katse kiran da yake mata, yasan ummi sarai yanzu kam bazata saurari komai ba, koma ta saurara zata ta kalubatanshi ne, don haka sai yace to Tashi ki bani abinci. Kin Tashi tayi don kanta jinsa take kamar ya fado, mi kewa yayi ya fita, ya rasa sukuni, koda yaje shago kasa yin komai yayi, sai murza hannunsa da ya mari ummi yake. Ya ciro wayarsa ya kira ummin tayi ta ringing kusan sau 3 kafin ummi ta daga yace haba ummi, inata kira kayi banza dani? Shiru dai tayi bata tanka ba, ummi cikin disashiyar murya tace, dama haka ne, sai an kwance ma mutum zane kasuwa azo gida ace za'a daura masa. Sai ta kashe wayar. Daga nan gidan umma ya nufa, tace anya Abba lafiyarka kuwa? Naga Duk ka ya mutse. Ya zauna suka gaisa yace umma ina fa lafia, dazun bayan sallar jumma'a ina iso wa gida da yunwa sai kurum na samu gidan tam d jama'a. Ummi da bishira na tarar suna ta zage zage har aka samu wata shedaniya taje ta kira umman bashar. Umma tace subhanallah! To ya akayi yanzu? Yace tarwatsa taron nayi, nasan koda ban tsaya bin bahasi ba ummi ce mai gaskiya. Domin bata kula bishira, Duk yarda akayi ta kure ta ne. Tsohuwa daga can gefe tace, wai bayan zuwa na gidan sukayi fadan? Abba yace oho ni ban masan mafarin fadan ba. Umma tace kai wannan abu allah ya dai dai ta maka su.

Amman kyanshi kana zuwa ummin ya kamata kayi wa fada, koma ka zane ta, don itace karama. Abba har suna hada baki da Tsohuwa gurin fadin "Haba dai". Abba yace umma in itace da gaskiya kuma ai na zalinceta, yanzun da haka fushi take, Duk na tsorata bana son fushinta, sai taki cin abinci. Don allah umma bari in kira maki ita ki bata hnkr, umma tace ba zan bata hnkr ba, abinci kuwa kada allah yasa taci. Sai dai ayi tunanin abinda ke cikin ta, Tsohuwa tace, wannan sakaryar matar taka dama na lura fada takeji. Sanda nayi sallama tana zaune amman amsawa ta gagareta, don haka ma ko gaisheta banyi ba na wuce. Ita kuma takwara ka hanata saka wadannan kayan na arna. Abba yace, su ake yayi Tsohuwa, Tsohuwa tace, tafdi lallai yayi ya zama banza. Abba yake cewa Don allah umma ga nmbr bari in saka maki a waya, ya dauki wayar umma ya saka mata lambar wayar da ke hannun ummin, yace umma na roke ki lallasheta ba wai fada zaki mata ZURFIN CIKI book 4 part 17
ZURFIN CIKI book 4 part 17
Posted by Bashir Sani Fesan on 15 Dec 2016 - 02:17
Duk jumma'a abba yana dawowa gida musamman in ranar girkin ummi ne don cin abinci na musamman. Jumma'a biyu kenan bata fado kanta ba sai wannan, don haka tun alhamis taje ta yarfo kitsonta, ta biyo ta gidan su gurin tsohuwa tazo. Don haka suna gaisawa da umma tace gurin tsohuwa nazo. Suka shige daki tace da tsohuwa nazo ne indan samu dan wani sirrin. Tsohuwa tace, name ummi? Ta ce na gyaran jiki mana. Fati tace min kwanaki kin fada mata wasu abubuwa. Tsohuwa ta ce, ja'ira, kinga uwar bari? Dama nace zaki same ni ina kyakkyawan zamana, bada ina fada miki kina sharewa ba? Ummi tace haba tsohuwa banaso aji mu yanzun dai ki bani shawara sannan ki fada min abinda zanyi inja hankalin mijina. Ta ce, toda farko ki dinga kula da jikinki ta hanyar rufe shi ruf, kada kibar kofar iska. Banda tafiya ba takalmi, iska tana shiga tanan kuma mace narage ni'ima banda zama ba dankwali inso samu ne hatta tsarki ki daina yi da

ruwan sanyi, ki dinga yida ruwan dumi. Sannan ki amshi bagaruwa gurin ummarki ki dinga shiga inkin tafasa da alif dakuma saiwar mata, sannan inkinyi al'ada kin gama kinyi wanka toki dinga matsa farin miski a ehem dinki. Sannan ki samu saiwar kankana, saiwar zogale, kanunfari, mazarkwaila dazuma amma kisa kanunfari dayawa sai ki dafa su su dafu kullum kisha kofi biyu safe da yamma. Sannan ki aya garinta, kwakwa ma kiyi garinta, dabino ma kiyi garinsa, sai ki dinga diban cokali bibbiyu ki zuba amadarar ruwa sannan ki zuba zumarki mai kyau kisha, sai ki samu kuma gwanda, kankana, abarba, zogale, citta, lemun tsami, ki markada su kisha. In anan maki katsaya yarinya zakiji ki kin cika cindum daruwan ni'ima sai kin samu martaba ta musamman agurin miji dan zaijiki kin fita daban da dukkan sauran mata. Ki hada da biyayya tsafta da kuma iya tsara girki mai dadi. Ummi tace, toni yanzun yaya zanyi nasamu saiwoyin nan? Tace, bari zanba matar ado dake yawan zuwa kasuwar qauye zata zo miki dasu. Amma su gwanda gasu nan bakin titi ko shi sai kice ya siyo miki, zogale kuwa baki rasa shi gurin ummarki, har da cittar da alif din da bagaruwan. Ta ce to, ta tafi gurin umma ta amsa har taje gida bata daina mamakin tsohuwa ba, ya akayi tasan duk wadannan hadin matan? Tun ranar alhamis din ta soma aiwatar da darussan da ta debo daga tsohuwa, safiyar jumma'a ranar zai bar dakin bishira. Ya fito tana sharar tsakar gida ta gaidashi, ya amsa da fara'a, tare dawani kallo mai fassarar in ba keba. Cikin muryar data adana don shi kadai tace, ya abba ina son in je ayi min zanen fulawa. Yace jiya kin fita yau kam a'a. amma ki aika akira mai zanen tazo ta miki. Ta marairaice, towa zan aika yaya abba? Yace aike ni, ina ne gidan? Tace layin su umma ne yace to za'azo ai miki. Bishira tafito daga daki tazabga ma ummi harara, Tare dacewa kisisina. Abba yakalleta, kema sai tayi miki. Tace bana bukata, aikin banza, shikam yafice. Ummi kuwa tace gaba da aikinta, ita ko sai tasa kujera tazauna tana

sakin zantuka, eh don kwalliyar tabanzanta tunda ba a iya biyawa miji bukata. Allah dai yasa ya fada min komai, to ni me zai dame ni don 'yar aiki kawai na dauki yarinya. Tashare min gida, tayi wa mijina abinci, daga nan fa? Saita saki shewa, ummi ta ce aranta yau zan bambance miki. Birabiskon shinkafa tayi da miya, ta wadata birabiskon da kayan lambu, miyar ta dauki nama da bushasshen kifi. Sannan ta hada musu kunun aya yaji dabino da madara, ta aikawa ummanta lokacin da kamal yazo daukar na ummarsu. Tasheka wanka taci doguwar rigar shadda koriya mai duhu, ta kafe dauri tamkar yau ne daurin aurensu. Ga fulawar da yaje ya biya akazo aka zana mata. Tanajin rigimar muhibba tafito tazuba mata adan kwano tazaunar da ita akofar falon mamanta. bishira tafito kicin baki tasaki tana kallon ummi da tazo wucewa harda bangazar ummi, nan ko kamshi ya bude ta na turarukan da ummi ta fesa. Abba yana yin sallama ummi tafito da sauri, oyoyo yayana, bishira tana daga kicin dinta tana kallon su. Ummi ta rungume shi, sannu dazuwa sahibina. Ta amshi ledar hannunshi dajakar, yace yauwa sannu babyna tace inazan kai ledar? Yace akwai ta bishira aciki ki ciro. Ta mika mishi ledar ta wuce dajakar dakinta. Ya mika wa bishira lemo da abarba da yayo musu tsaraba sannan ya wuce danasu, awulakance ta aje. Yana shiga ummi tadan karo kofar yanda bishiran zata iya lekensu sosai ta gefen kofan. Ta cire masa hula ta aje akan madubi sannan ta kunna fanka. Ta shirya masa abinci, yauni zan baka har ka qoshi. Haka suka yita baiwa juna abaki har suka qoshi. Yakamo hannunta mai qunshi yana ta sumbata, wai kamar kada su goge. Kumatun shi ta shafa nima yau kamin kyau, koda yake dama kai me kyaune, ina sonka ya abba sosai. Cikin jin dadi ya mannota a jikinshi, nima ina sonki, ina manta kowa da komai in muna tare, tace ina tsoron kada wata rana ka juya min baya. Ya saqalo hunnuwansa cikin nata ina fata in mutu kafin lokacin. Ummi tasomayi masa wasu irin darussa wadanda tasan yana

saurin tada sha'awarshi nanda nan kuwa tasa shi fita hayyacinsa yakama surutai. Ummi ta tabbata bishira tana wurin ta labe, don haka tai murmushi ta bishi suka tafi duniyar ma'aurata. Bishira tamkar tayi hauka sai kawai ta fado dakin tana fadin, maciya amana, har yanzun ba afita daga lokacin girkina ba munafiki. Abba ya tashi sannan yaja riga yasaka, ok dama kina labewa ne kiji sirrinmu? Da taga ya sauko da zafin rai saita gudu dakinta. Yabita yamata tatas, kuma ya fada mata cewa tazo ta shiga dakin ta zauna ba labe ba, yanzun zai komane yaci gaba daga inda ya tsaya. Tayi ta kuka gashi ba damar zuwa gurin umman bashir dole ta tafi gidansu. Shi kam abba shareta ya yi kosu umma bai fadawa ba. Sabuwar soyayya ma ya balle agidan, su ci abinci tare, wanka tare, su fita yawonsu a qafa ko amota. In yana gurin aiki bini- bini ya kira waya, ita kuma ko yaushe cikin kirkirar girki da kwalliya tare da dadadan kalaman dazata fada masa take.ZURFIN CIKI book 4 part 18
ZURFIN CIKI book 4 part 18
Posted by Bashir Sani Fesan on 15 Dec 2016 - 02:19
Ummi tayi alalar gwangwani ta sauke kenan sai ga aunty farida da yake tunda akayi auren ummi batazo gidan ba. Har daki ummi ta shiga suka gaisa tayi masu addu'a zama lafia, tayi mata nasihar zama da miji. Umman taji dadi tare da kwadayin ina ma bishira take da halin yayarta, ta zuba alala ta kaima aunty falon bishira. Ta isko su tana mata fadan kaxanta, cikin murna aunty ta anshi alalar taci bishira ta cika fam. Tun tana jurewa har tace aunty ai kin zubar min da kima, ya ya za'a yi ki anshi abun kishiya kici. Aunty ta kalli bishira fuska daure tace ke da ita akwai bambamci ne? Bishira tace aunty bambamci ma nifa jininki ce ita fa? Aunty tace a musulunci fa? Bishira ta hade rai tana kallon aunty, taci gaba da cewa, A musulunci tama fiki don tana sallah, Haka nima ina sallah, kefa kin faru? In kin soma sallar to kin shigo cikin mu ni da ita. Domin addinin mu ya nuna muna dukkan musulmi dan uwan musulmi ne. Inji mai tsira da aminci. Haka zan iya cin abincinta banci naki ba don bakida

tsafta. Ta daka mata tsawa tashi don allah malama kije kiyi wanka, ki wanke duk jirwayen nan naki kafin In daukeki da motata. Da zasu tafi har kudi aunty farida taba ummi, ummi kam godiya ta dinga yi. Haka nan da abba ya shigo ta nuna masa tace ai abba ya ciri tuta a zuri'arsu, halin mahaifinsu ne da ita. Wata rana aunty ta bugo ma abba waya cewa aisharsu ta haihu don allah ya fadama bishira koda ya iso gida ya fada mata nan ta shiga murna. Washe gari tace zata gida tama mahaifiyarsu barka. Sannan taji randa zasu abuja wurin aisha. Yace ta shirya ya sauketa, ta samu aunty tazo nan dai sukeyi wa juna barka, mahaifiyarsu tace dubi yar uwarki sai yanxu ta haihu gwanin shawa. Amman kinje kin gwarje miji ma yayi maki kishiya, dubeki kamar ba yar gidan nan ba. Aunty tace mummy ai ita taso ta zama Haka, tunda kaxanta ce sana'arta. Hajiya zainu tace ni wani lokacin bana ganin laifinta a kaxanta, don a gida bata saba aiki ba. Laifinta daya a gurina wannan abba data nace ta aura, data tsaya ta gama karatunta ta auri wanda zai dobo mata yan aiki komai saidai ayi mata tana daga zaune, amman ta likema talakan tela wanda bashida ko sisi. Aunty ta katse mamarsu da cewa In tana da yan aiki shine har wanka zasuyi? Ta cire dan kwalin dake kan bishira kalli fa mummy har kanta zasu wanke mata. Mummy tace aiki gida ya mata yawa, yaushe har ta gyara jikinta? Aunty tace kawai mummy kina goyon bayanta ne. Bishira tace aunty mummy ta fahimta kece baki fahimta ba saboda kina da yan aiki. Mummy tace duk ba kece kika yima kanki ba, ga kishiya an maki, bishira ta tabe baki nima duk nadama ta isheni. Kuma shi da matar duk bana raga masu. Don ban damu ya sakeni ba, yaji ne dai nace na daina, daddy ko nazo cin mutuncina yake gabansu. Mummy tace kin man dai dai. Haka yake bishira kullum cikin tsokanan hayaniya da ita da miji ko kishiya. Amman ummi yamxun bata kulata Domin umma ta gargadeta. Bishira bata bar gidan ba saida mummy ta zugata Sannan tace mata jibi kizo za a kai su innarku

yin barka abuja kije ki dan huta kafin suna. Bishira tace daman ban taba zuwa ba, ko anyi suna sai na huta. Aunty tace kada ku yanke hukunci ba tare da sanin mijinki ba kije kiji ta bakinsa. Bishira ta ce ina ruwana da yardarsa aunty. Haka kuwa data dawo ta shiga tattaro kayan ta dake jibge a gefen gadonta, don ita zane ko yau a aka dinka shi In tasa ta cire duk In da tayar kafin ta dauke shi yaji jiki. Wani ma saita goge ruwa ne, kamu ne, duk kyan zani saita goge tsakar daki dashi. Ranar dama abba dakinta yake, tace mashi jibi zamu abuja Inji mummy. Taso ya dan sai mata zani sabo wanda zata danci suna ya dinka mata. Yace akwai wani leshi dan sai maku yana shago, Tun wancan satin naso In zauna In dinkashi da kaina don mai tsada ne. Tace nawa ka siyeshi, yace dubu biyar ko wane daya, bishira ta tabe baki. Na zaci zakace sha biyar wai dubu biyar, yace matsalata da ke rainuwa yace bari zansa a dinka maku gobe ashe sunan har yazo? Tace a'a jiya pha ta haihu, ya sake kallonta jiya? Shine zaku tafi jibi? Tace eh mummy ce tace mu tafi jibi. Yace a'a kibari sai ana gobe suna kije. Kafin lokacin ma na samu wasu kudi da nike sa rai. Sai na sai maki kayan barka zanen maman da kayan baby. Bishira ta ce gaskia gobe zamu tafi, In ka sayi kayan barkar ka aika dasu can wurin mummy yan tafiya Ranar suna su kai mata. Abba yace nifa ban amince da tafiyar nan gobe ba. Ban yarda ba. Bishira ta ce ba wai ina neman yardarka bane, ina fada maka umurnin da mummy ta bani ne, ko ka mance mahaifiyata ce? Mamakinta ya cika abba, yace mahaifiyarki ita zata baki izinin tafiya ko ni? Umurnina da nata yanzu wanene...? Bishira ta katseshi kada kayi ganganci hada kanka da mahaifiyata, ita ta haifeni ta raineni har ka ganni kace kana sona Sannan ka dinga kokarin kwatanta kanka da ita? An fada maka kowa baisan darajar mahaifiyarsa ba irinka? Abba ya mike ni ne bansan darajar mahaifiyata ba? Tayi shiru yace nagode Kuma suna na hanashi ma gaba daya. Zan gani Kuma Bishira ta ce zako ka

gani.ls / ZURFIN CIKI book 4 part 19
ZURFIN CIKI book 4 part 19
Posted by Bashir Sani Fesan on 15 Dec 2016 - 14:14
Duk ummi tana jiyo su amman bata fito ba, tana ta mamakin yarda bishira batasan darajar aurenta ba, bare tasan girman miji. Ranar da zasu tafi kuwa ko a jikinta ta dibi tsummanta ta nufi gidan su, Duk ta fadama mummy yarda sukayi. Mummy tace kinman dai dai talakan banza shine zai hada kanshi dani, tafiya zakiyi in yaso in kika dawo ya ce baya auren. Abba ya dawo ya samu dakinta a rufe, ummi na daka sakwara a kofar dakinta yace ina bishira? Ummi tace ina ga ta fita, don ina daki bansan fitarta ba. Ya daga waya ya kira aunty yace bishira tazo? Aunty tace bata fada maka zasu tafi abuja bane, Abba yace ta fadaman amman nace a'a sai ana gobe suna zataje, ya kwashe komai ya fadama aunty. Aunty tace kayi hnkr don allah idan ta dawo da kaina zan hadata da daddyn mu, Abba yace kiyi hnkr aunty na gaji da halin bishira inga wannan karo gwara kowa ya huta ni da ita. Aunty tace kayi hnkr Abba yace sai anjima ya kashe wayarsa. Zama yayi kan kujera dakin ummi yace gaskia wannan karo bazai fadawa kowa ba ya gama auren bishira. In bai nuna mata kurenta ba nan gaba zata masa abunda yafi wannan don Haka yabar komai sai ta dawo. Ummi kam batason ya rabu da matarsa, amman kam saida taga tarairaya cikin kwanu kan nan matsalarsu daya, Abba yace ummi kodai asibiti zamuje ne, ummi tace muce masu mi? Yace muyi masu bayani mana, ummi tace a'a. Yace to muje mu fadawa umma, ummi ta zare ido yanxu sai kama umma wannan zancen? Yayi murmushi. Ai da zan iya mata wannan maganar da tuni na mata, asibiti ma abunda yasa banson zuwa sai likita ya bukaci ganin wurin. Ni kuma ina kishin wani namiji ya kallan mi al'aurarki, ummi tace nima ai shine, ya sake janyota jikinshi. Yanzun Haka zamu zauna? Shine nakeson in fada maka naji kana ka gaji da aunty bishira kila zaka saketa ne. Toh don allah ka rabu da ita tunda ko ka saketa

sai ka auri wata. Tunda nasan zama Haka bazai yiwu ba. Ta soma hawaye ya shiga lallashinta yace Allah zai yaye masu. Haka sukaci gaba da rayuwa cikin kwanakin da bishira bata nan, ummi tanason kalolin wasanin da Abba ke mata, amman da yaso kwatantawa ko allah ya amshi addu'a su ta warke saita kwace jikinta ya hau bari tayi ta kuka. Don Haka sai ya hnkr da bukatarsa amman ya takura sosai, kuma yana ganin dole yabar batun bishira yanxu don Haka ya jaye batun saki amman sai dole ya nuna mata kurenta. Ranar data dawo kwananta takwas Ranar ma bata da niyar dawowa sai da aunty ta kira mahaifinsu ta sanar dashi, ya kirasu a waya ya zagesu tas gaban mahaifiyarsu harda mai jego. Tace bishira ta dawo shine ya kira Abba da waya ya bashi hnkr yace Duk irin wannan ta faru ya kirashi ya sanar dashi. Abba ya shigo da T. V guda 2 daya ya kai dakin ummi, daya ya kai falon bishira wanda ya yanke kwadon. Ummi tayi ta murna bishira kuma ta daki Duk rashin kunyarta gabanta sai faduwa yake, batasan ya zasu kwashe ba. Sai da taga baiko kalleta ba daga ita har yar sannan ta dan saki jikinta, tasan ba zai tsaya a fushi ne in taci sa'a. An dauki sati guda Abba baya ko kallon inda bishira ta ke ko Ranar girkinta sai dai yayi kwanciyarsa a falonta. Duk da yana bukatarta Haka kuma ya janye yan wasanin da yake da ummi don wahalce yake bacci, ita kuma sai ta damu don ya saba mata sai tayi tunanin ko laifin tayi masa ne. Ita kam bishira ganin zura ido ba zai kaita ba, don Haka ta sauke zafin kai ta iske Abba a falonta wani dare harda kukanta take bashi hnkr. Wai sherin shedan ne ba zata sake ba, Abba ya dubeta mi kikayi? Tace nidai ka yafeman, yace ashe kinsan kinyi ba dai dai ba? Ai inda ke ce saikin kara, amman bari kiji na rantse maki duk kika kara zuwa wani wurin bada izinina ba wllhi sai kinsha mamaki. Tace na yarda, abun mata da miji nan dai suka sasanta, hakan nan dakin ta ya kwana, suna shiri cikin satin don bishira ta fahimci mijnta ita kadai a matarsa, yarda yake rawar jiki lokacin

kwanciyarsu. ***ummi na zaune idonta kan tv Abba take kallo yarda yake watso turanci cikin kwarewa. Kullum kara sonshi take, ta kwantar da kanta a hannun kujera, kusan sati guda kenan tana lura da Abba. Baya son ko taba hannunta sannan ga wani shiri da yake da matarsa, sai dai yazo yaci abinci ya dauki laptop dinsa ya raba dare. Inko yazo kwanciya saidai ya juya mata baya sabanin kwanaki da yake mata makwanci da hakarkarinsa, lokacin tasan babu inda keda dadin kwanciya ga matar aure irin hakarkarin mijinta, sam bata iya bacci sai tunanin abunda tayi masa, amman yau din nan zata tmbysa ko laifi tayi masa, Bayan yaci abinci yayi wanka ta dauko mai zata shafa masa ya amsa da murmushi yace barshi kawai nagode, ta dawo ta zauna, zaya fita tace ina zaka ya Abba, yace aski zani, ko zaki rakkani tace eh yace taso muje. Suna tafe suna hirar aikin shi, yace An koma kirkirar wani filin kuma An saka shi ciki, yanxu abubuwa zasu kara mashi yawa. Sun isa babu layi An suma mashi ya mika mata wayoyinsa guda biyu tana danne danne kira ya shigo. Nan take ta hade rai ganin sunan dake jiki zainab dina, ya tmbyta da ido waya kira ta sake hade rai, sannan ta mika masa. Ya kalli sunan zainab sannan ya daga cike da son ya zolayi ummi yace zainabuna. Can bangaren Duk da kallaman Sun mata dadi tace da ba amman yanxu ta wani ce. Yaya salis ya kawo maka katin aurena? Yace eh yabani tace ya amarya? Yace gata bari in bata ku gaisa, ummi ta kauda kai tare da jan tsaki, yayi dan murmushi yanason yanda ummi ke nuna kishinsa, salon da take wurin kishinta daban ne. Yace zainab Wai tana gaisheki, zainab tace to ina amsawa. Ka gaida umma sannan ka sai masu anko kalla biyu ne. Abba ya naji ko kalla goma ne zan saya tace to gobe kazo gidan mu nan ake sai dawa. Ya kalli ummi yasan kadan ya rage ya kaita bango. Ya danne dariyar da ta taso masa yace gobe kikeso nazo gidanku zainab? Tace eh don gobe za'a kawo wasu kayan, yace to zanzo, ummi ta zaro ido ta mika tsaye dai dai lokacin da aka gama

askin. Yayi sallama da zainab din sannan ya shiga karkabe jikinsa. Ummi kam tuni ta kai bakin kofa. Ya sallami mai askin ya isketa Sun jera yanxu ba kamar daxun da suke fira ba. Sun kusa layinsu yace muje mu gaida su umma tace ni bacci nakeji baice komai ba, Sun iso hijabi kawai ta cire ta kwanta, yace Wai lafia don zainab ta kirani tun dazun kin kasa sukuni?URFIN CIKI book 4 part 20

ZURFIN CIKI book 4 part 20

Posted by Bashir Sani Fesan on 15 Dec 2016 - 14:17

Ummi ta taba baki, Allah yakawo ta lpy. Ya ce ni ban soba gsky. Sbd ke ummi tadafa kirji, sbd ni? Ni ya abba, kada kasa duniya ta zage ni, Tare fa nasameku? Yace to ni dai kada kiga kamar da son raina, tace don Allah ya Abba kabar zancen nan. Kaje kagyar mata dakunanta don su kamal bazasu iya ba, yanufi gurinsu ganin kamar ya damu yasa itama taje tasa musu hannu don dai ya saki ranshi, sun gyara tsaf ummi ta goge sannan ta rufe dakin. Har magriba bishira bata ji an ce za'a maida taba, sai ta dauki wayar kanwarta ta kira shi wai yazo don Allah yadauketa. Tsakanin mata da miji sai Allah, nan ya tausaya mata yace zaizo, kafin ya isa sai daya sai mata waya irin dai ta hannun ummi. Har cikin gidan ya shiga suka gaisa da babanta, yayi murna sosai yayi tawa Abba godiya, tare da ba shi hakuri yace yasan yanda ta horu zai gata canza da yardar Allah. Yasa aka turo ta yayi mata nasiha, sannan ya gargadeta da cewa inhar ta bari mijinta yakawa kararta zatayi mamakin abinda zai mata. Tace, insha Allahu baza ta kara ba, yakawo kudi yaba Abba, da kyar ya amsa ita kuma ya bata wasu zannuwa acikin leda, yace su raba da abokiya zamanta. Taje tayi wa hajiya zainu sallama suka tafi, tamkar baquwa haka ta koma, sai kace basu taba zaman aure da Abba ba, nauyinsa take ji. Suna tafe ya ciro waya ya miqa mata, tasa hannu ta amsa yace taki ce, tayi ta godiya yace ba komai. Sallamarsu tasa gaban ummi faduwa, ta dake ta fito ta amsa, wani kishi ya tasho mata amma saita danne. Ta kalli bishira tare dayi mata sannu dazuwa, ta amsa tana

kallon ummi tayi kyau tagoge daga ka ganta kaga wayayya 'yar gatan miji. Ta dauko makullin dakin ta ba bishira, abba kuma ya nufi dakin ummi. Bishira ta dinga kallon yanda abba ya gyara gidan yaja gini ta gefen ummi yayi mata falo da kicin, sannan tsakar gidan an gyare shi da tiles. Haka bandakin su yagyara shi, nan dai bishira ta shiga dakinta ta zauna bakin gado tana yi wa allah godiya tare dayi wa kanta alkawarin har abada bazata ta kara yin yaji ko ta janyo abinda zaisa mijinta ya sake ta ba. Ummi tana kan gado tana karanta wani littafi yazo ya zauna bakin gadon bata ko kalle shi ba don haushi take ji. Sai take ganin kamar rawar kai yake yi da dawowar bishiran, kuma tuntuni yana zuwa gurin ta ya boye mata. Yace madam ina son in yi magana da ku ne ke da bishira, ummi tace ina jin ka, yace can zaki zo muje. Tace, gsky nagaji, kayi maganar da safe. Yagama gano kishi ne ke damunta, don haka yayi murmushi yace yanda kikace hakan za'ayi. Ya fita kamar minti 30 yasake shigowa ya aje mata leda tare da cewa saida safe aciki tace Allah yabamu alheri. Yana tafiya taje ta banko kofarta, yau kam bacci ya qi idanun ummi sbd tayi sabon bacci a haqarqarin Abba. Dukkan filolinta ta rasa wanda zai maye mata madadin haqarqarin mijinta, ynzun yancan da wata tasan yanda yake wannan rawar jikin ynzun ya manta da batunta. Tarasa me yake mata dadi, littafin datake karantawa kuwa sam bata fahimtar abinda ke ciki. Hka ta dinga zubda hawaye har nisan dare, ganin bata da wata mafita, tashi tayi ta bude kofa lokacin 2 saura taje tayo alwala tazo ta kama nafila. Abba jin bude kofarta ne yasa shi leqowa ta window aranshi yaji tausayinta don yasan bata iya bacci sai ajikinshi, ita bata san ya leqo ba don ko hanyar dakin bata ishe ta kallo ba. Yakalli bishira wadda bacci yayi gaba da ita ya tausaya mata sosai yanda tayi tarawar jiki alokacin auratayyarsu dazun. Yadauko wayarshi yarubuta ma ummi sako. KI KWANTA KIYI BACCI BABY, TARE DA QISIMA CEWA KINA LAFE

AMAKWANCINKI (WATO JIKINA) INA CIKE DA KEWAR LEBUNANKI Tana sallah taji shigowar saqo amma bata yi ko marmarin dubawa ba, haka tai sallah har zuwa lokacin da bacci yasoma fizgarta. Tayi adduo'o'i sannan ta kwanta, saida asubahi ne datayi sallah sannan ta karanta, dan tsaki taja tare da cewa, Karya kawai, kishi yasa ta fadin haka don tasan Abba sosai baya boye mata komai ynzun. Sai dai abinda yasake qular da ita da asubahin nan yanda tana fita shi kuma ya fito wanka, duk da tasan dole wani abu yafaru tsakaninshi damatarsa, amma sai taga tamkar da gayya ya tsaya don tafito taganshi. Tna idar da sallah ta dora ruwa akicin dinta, tadafa ruwan tea taje kicin din bishira tadauko flask tazo ta wanke ta zuba musu ruwan zafi taje kofar bishira tayi sallama bishiran ce ta bude ummi tamiqa mata tare da cewa an tashi Ipy? Cikin sakin fuska tace, Ipy lau, nagode. Ummi ta ce ba komai takoma dakinta ta kulle kofarta don yau bata da darasin safe. Abba ma yau bada wuri zai fita ba, don haka yadan samu baccin safe sai 8 yayi wanka ya karya, sannan yanufi dakin ummi. Kofarta tana rufe, ya kwankwasa ta share sai can dai dataji yaqi tafiya sannan tazo tabude. Takalle shiya yi kyau cikin kananan kaya, ta kauda kai tare da cewa, an tashi Ipy? Yace Ipy lau, kin karya? Tace, um'um sai anjima, zata rufe kofar yace, makaranta fa? Tace sai karfe 2 nake da darasi. Ta maida kofar ta rufe, yayi dan murmushin takaici sannan yafita. Kwananshi 2 dakin bishira yayi niyyar dawowa dakin ummi, don ya kosa yadawo ya lallasheta bazai iya daukar wannan shariyar da take mishiba. Tsakaninta da bishira Ipy lau amma shi sai tana wani share shi. Ya shigo da zumudi zai nufi dakinta, tamiqe cikin fara'a daga wanke-wanken da take yi ta amshi ledar hannunsa da jakar laptop ta nufi dakin bishira. Shida bishira suka bita da kallo, ganin zata shiga bishira tace ummi yau ai dakinki yake. Ummi tace injiwa? Anty bishara ai kullum ke ce dashi har sai kin rama duk kwanakin da kika dauka agida. Kinga kenan kusan wata goma sha

daya kenan. Abba cikin sauri yace ke mahaukaciya ce? Ina ki kasamo wannan fatawar? Ta kalle shi, sannan tashiga dakin ta ajiye ta fito taqara kallonshi gurin malamai, yace to ban yarda ba, don haka zanci gaba dayi muku kwana bibbiyunku, ummi tace to ni na yafe mata nawa kwanakin bishira tace nagode ummi. Haushi ya cika Abba, amma shi bazai dauki wannan horon da ummi take shirin yi masa ba. Yadawo dakin bishira a fili yafurta kema saina baki haushi zakiyi dakin sanin wannan furucin. Sharewa yayi yaci gaba da kwana dakin bishira tare da nuna kulawa ga bishiran. Ummi ta jure duk da duk daren Allah sai taci kuka ta gode Allah, sannan tashiga zargin cewa shi ma ya Abban dama can yana son tarewa dakin bishira, inba haka bame zaisa yayi saurin yarda kuma yayi ta nuna mata soyayya? Ganin ummi tana yi tamkar bata damu ba yasa shi qa rajin haushi, yadawo da yamma suna zaune kowa A qofarshi. Ummi tayi kwalliya cikin qananan kaya, bishira kuma tana sanye da leshi, karatun littafi bishiran keyi ita kuma ummi tana yin gyaran qumbunanta. Bawai suna wata hira bane amma suna kula juna sosai musamman bishira tana son su saba da ummi. Ummin ce. bata cika son fitowa ba, bishira ta tashi ta masa sannu dazuwa tare da amsar kayan hannunsa don yanzun tana koyi da ummi gurin kyautatawa, ummi ta kalle shi sannu dazuwa, ya amsa da yauwa baby. Yakalli bishira sweety zanyi wanka, tace to, takai masa ruwa yashiga dakinta, sai tazo tace masa takai nan k sweety zanyi wanka, tace to, takai masa ruwa yashiga dakinta, sai tazo tace masa takai nan kuma yajanyo bishira jikinshi. Ba wai yana da bukata bane, amma don ya shaqar da ummi sai ya banko kofar, qaran kofar ne yasa ummi kallon gurin dakin. Ta duqar dakai taci gaba da abinda take yi, kusan minti arba'in suka fito, Abba ya matsawa bishira wai suyi wanka tare, tace ni bazan iya ba akwai ummi dama da dare ne inajin kunya. Kuma kada taga kamar cin fuska ne, yace kenan don kada ki bata mata rai ni mijinki bazaki faranta min ba ko? Dole

ta bishi suka shiga bayi. Baqin ciki yasa ummi tashi tashige daki, kuka sosai tayi daga nan bata fito ba sai magriba, tanayin alwala tarufo kofa, washegari ma qin bude qofar tayi daga alwalar asubahi. Abba yayi ta raba ido ya ganta amma bata fito ba, yasan fushi take, ya kira wayarta taqi dagowa yayi mata saqo cewa in zata makaranta tafito inkuma sai darana ta bude ta amshi kudin mota. Tana gama karantawa tayi wuri da wayar ba tare data bashi amsa ba, haka ya tafi. Bishira ta qwanqwasa ma ummi ta bude suka gaisa, tace naga baki fito bane ina fata lpy? Tace lpy lau bacci ne, tace yau baza kije makaranta bane? Ummi tace, zanje sai sha biyu. Bishira tace kinji dadinki ni gashi nan ina tayi masa zancen karatun amma ya share ni, ummi tace inkin matsa zai yarda, tace ko za ki dan sa min baki? Ummi ta riqe baki, ni a wa? Ke da yake hannunki ai ke ce zai saurara, ni kin zo ne ma ki zage ni. Bishira tace wane irin zagi? Ni dama ki amshi mijinki ummi don gangar jikinshi ce kawai agurina, amma ruhinsa yana gurinki. Ummi ta ce, ngd da zagi, bishira ta ce zancan gsky ne ba wani zagi. Haka suka yi ta rayuwa cikin kwanakin ummi kam har rama tayi shima Abba ya rage walwala don wanda yasan kan kula da shi kamarta. Yayi missing din abincinta. Amma ya gaji bazai jure ba. Ya tuna bishira tace masa zata ta yini gidan ummanshi. Don haka yana gama muhimman abubuwan da zai yi agurin aikin yanufi gida. Ummi tana shirin tafiya makaranta ta dauko jakarta sai kurum taga mutum kamar an jeho shi. Ta daure fuska tamkar bata taba dariya ba, yace ummi nagaji kin ji ko, na gaji da wannan horon naki. Laifin me nayi miki? In don na dawo da bishira ne sai in saketa, duk ba kece kika takura min sai na dawo da ita ba? Ummi tace, ni karka doran jakar tsaba kasa kaji su bini, ka saki matarka sbd ni? Ba ruwana. Yace, to ki dawo yanda kike, kuma ki janye batunki na wai kin haqura dani, niban haqura ba. Ke ma kuma nasan dole ki kasa kanki, ummi ta ce ni ban damu ba, ya ce qarya ne gashi nan duk kin rame? Ya

canza daga fada zuwa lallashi, ummi don Allah na roqeki mu koma kamar da, haba bebyna. Ya lalubo hannunta ta qwace, don Allah ka tafi kada bishira ta dawo ta same ka anan ta zargi wani abu. Haushi yakamashi sosai, ya daga murya da qarfi, kin san Allah ummi zan hadaki da umma, ta nufi hanya fita, nikaga kada kasa ni yi latti don lokaci yayi nisa. Ya ficiko ta ta dawo ba zaki makarantar ba, ke an ma daina karatun tunda yafi ni. Ta zubar da jakar da hijabi ta nufi gado shi kuma ya fita cikin zafin rai, gidan su umma yaje. Bishira tana dakin umma tana sallah yabi umma kicin, umma gurinki nazo, ta dube shi lafiya Abba? Ya turo baki, alamun ranshi bace baki, yace umma ki sallami bishira, tace kamar yaya? Yace taje can gidan ko muyi maganar agabanta? Tace, kyale ta muje dakin babanku. Abba ya fada ma umma komai da ummi ke masa, tun dawowar bishira ran umma ya baci tace ka barni da ita. Banda shashancin ta da ita kadai take son azauna? Baga bishirar nan ba gidan nan ta gane kuskurenta ko yau yarinyar nan sai da tace in yafe ta nace ni dama ban riqe ta da wani abu ba. Shine ita zata qirqiro fitina? Yace, umma ai ba da bishira take yi ba dani take yi, tace to zata gane kurenta da dare kuzo kai da ita. Umma ce ta kira ta awaya tace tazo ita da abba, jikinta ya mutu don tasan qararta aka kai, tana idar da sallar isha'i taje gidan. Can tasamu abba, nan ko umma ta rufe tada fada, koda tsohuwa ta jiyo tazo umma tafada mata komai sai ta shiga fada. Wai ai kishi halas ne, ke suwaiba tsakani ga Allah ko ke bazaki so kishiya ba, bare ita yarinya. Abba yace to gata nan ita ce fata dame ne nida batun in dawo da bishirar, yanzun na dawo da ita kuma ni abin ya qare akaina? Nan fa umma tayi mata tatas, ta kuma sata anan ta ba Abba Haquri, aka kira shi awaya ya fita. Umma ta samu dama taqara yi mata nasiha da cewa, in bnda shirmenki yaushe zaki bar ladanki, hanyar aljannarki kice kinyi fushi da ita kin barwa kishiya? To kada in sake jin haka, ki riqe darajarki da mijinki, ke ganinki da ita. Ta jima tana bata shawara kafin

Abba yadawo suka nufi gida. Ya shiga gurin Bishira ya fada mata cewa yau gurin ummi zai kwana, nan ya bar ta da kewa yanufi gurin ummi, tamkar yaune daren farkonsu hara sukai rayuwa s / ZURFIN CIKI book 4 part 21
ZURFIN CIKI book 4 part 21
Posted by Bashir Sani Fesan on 15 Dec 2016 - 14:19
Kwanci tashi asarar mai rai, shekara ta zagayo lokacin bishira da tsohon ciki, Abba nason yara don muhibba taqi dawowa tafi son umma dole suka haqura suka bar mata. Ta haifi 'yarta budurwa tubarkalla ranar suna ta ci sunan sahura inda suka sa mata walida. Ummi nason yara, don haka in tana gida to tana manne da walida, Abba yana damuwa da rashin samun cikin ummi, wanda ita ummin ta barma Allah komai. Shekaru uku sun sake biyo baya, lokacin Bishira ta sake haihuwar habiba takwara Abba yayi wa ummi. Tsohuwa an qara tsufa, 'yan rigingimu sun qaru tace ita Abba yama takwara amma bata son ya duke ta irin yanda yayi wa ummi. Abba kullum qara son ummi yake, umma ta matsa masa sai da yayi qoqari ya sai fili rabin filoti tace kuma a rage ciye ciyen dadin nan agina shì. Haka kuwa ya gina flat mai daki hudu, daya ummi daya bishira, sai nashi sannan na yara. Yayi qoqari gurin gyaran falon ita kuma ummi ya canza mata kayan daki don bishira an canza mata daza su tashi agidan su. Yace tabishi bashi in ya samu zai bata kudi amadadin kayan daya saima ummi, tace ta yafe. Ummi dake karantar (BUSSINESS) har ta hada (H.N.D) dinta kuma tayi bautar qasa. Abba dai yace baza'ayi aiki ba amma ya yarda tayi kasuwanci, Alhaji babba ne ya bata jari inda take saro kaya zannuwa, lesuna, takalma zuwa jakunkuna. Abin ya amsheta don har kayan aure tana hadawa, tana yin saqo irin su kwatano da chaina, india, pakistan ko dubai, ta hanyar wani wan kawarta. Haka kawai ummi ta samu kanta da zaban abinci, yawan bacci kasala da dai sauransu, sam bata san takamaiman lokacin al'adarta ba. Don bata wani lissafi in yazo shi kenan in bai zo ba bata damu ba tama cire ranta

daga batun ciki. Abba ya kalli nonuwanta, baby kwanan nan kirjinki ya cika sosai, gashi kinyi haske ko kin canza mai ne? Tace yaya yaushe kazama likita? Yace, ummi kin fa canza shirya muje asibiti, ta ce ya Abba don Allah ka bar ni nagaji dazuwa asibiti. Yace, to ni zan je inya tambaya game da yanda ki ka canza. Cikin jin haushi tace sai ka dawo. Ga yara atsakar gida sun ishe mu, yace ni naki nake qawar in gani nasan addu'ar da nike yi bazata fadi kara banza ba, sannan ga qoqarin danake yi, shiru ta masa. Dagaske yake yi yaje yayi wa likita bayani, yace yadai kawo fitsarinta. Sai da suka yi tsiya da qyar bishira ta lallasheta ta yarda ta bada fitsarinURFIN CIKI book 4 part 23

ZURFIN CIKI book 4 part 23

Posted by Bashir Sani Fesan on 15 Dec 2016 - 14:22

Sam bishira bata damu da barin mijinta da zatayi gurin ummi ba, tunda ta jima da sanin cewa ummi bata da wani ammafni. Wannan ne ma yasa tasha alwashin in taje zatayi addu'a Allah yakara toshe ummin kada ta warke sam, tunda umma Bashir ta fada mata duk addu'ar da tayo kafin ta dawo an karba mata. Ta kuma kara bata shawara ta roko musu rigima suyi tayi har su rabu, Bishira tace duk zata roko. Ko ranar da zasu tafi sai da ta yi wa ummi habaici, kawyenta sun shigo wato makotansu a tsakar gida take fada musu cewa mijinta kurum take tunani. Wai zai sha wahala kafin ta dawo. Wata cikin su tace, wahalar me ga shi da amarya? Ta ce amaryar da ta ke a toshe, ai bata da ammfani. Ummi duk tana ji, takaicin duniya ya isheta sai dai ita zata so ace bishiran take ta roko ma kanta shiriya ko Allah zai sa ta dawo ta kama sallah. Dayar tace, to Bishira ki roko mata sauki mana, cikin zolaya tayi zancen, Bishira tace ba abinda zai kaini makka in roko ma kishiya abin arziki. Ummi ta fito ta ce Anty Bishira zai fi kyau ki roko ma kanki shirya ko in kin dawo kya fara sallah da tsafta. To ban san ma yanda zaki kwashe da ibadar ba ko za a karba tunda ba yin sallah ki ke ba. Ta taso fuuu, kawayen suka reketa suka ce kyaleta bakin ciki ne. Abba ya fito wanka yana

cewa, Ok, za kuyi na bankwana ko? Yana da kyau hakan. Ummi ta koma dakinta. Tun bayan tafiyar Bishira Abba ya shiga takura musamman irin wannan lkc na sanyi. Ya dawo da yiwa ummi 'yan wasanni da ya daina, sai hakan yakara sa shi damuwa don haka ya shiga lallashin ummi ta fadawa umma....... Kuyi hkr da typing din banda lafia sstr dita nake sawa tana maku.els / ZURFIN CIKI book 4 part 24

ZURFIN CIKI book 4 part 24

Posted by Bashir Sani Fesan on 15 Dec 2016 - 14:24

Tace ita kam ba zata iya ba ranar wata juma'a suka tafi da nufun su fadama umma matsalarsu, sai dai har zuwa bayan isha'i da abban yazo don su tafi sun kssa sanar da umman komai, har sunyi sallama abba yayi kunar bakin wake yace umma ta fada maki matsalarta? Umma tace wa? Yace ummi tace a'a suka koma suka zauna. Abba kanshi na kasa Yace umma dama bata da lafiya ne? Umma tace mike damunta kuma? Yace ummi fada mata. Ummi ta sunne kai cikin cinya tare da cewa shiya fada. Cikin sa'a aka kira wayarshi, nan yayi waje ya barsu, umma tasa ummi saita fada. Ummi ta rasa ta inda zata dauki zancen, umma ta soma yi mata fada har tsohuwa ta leko tambaya take lafiya ba sunyi sallama dama basu tafi bane? Umma tace wai bata da lafiya ne, kuma ita da abban sun kasa fadaman shi yayi waje, ita kuma ta kunshe kai cikin cinya wai injira ya dawo ya fadaman. Tsohuwa taja hannun ummi zuwa dakinta, suka zauna bakin gado ta riko hannunta. Takwara fadaman abunda ke damunki. Ummi ta sunkuyar da kai ta kasa magana. Tsohuwa tace inda baki fadaman ba akwai wanda zai taimaka maki ne? Tunda naga duk yarda mijinki yake da umman ku ya kasa fadamata to abun mai girma ne. Ummi ta daure tace "Gabana ne fa a toshe....." tsohuwa ta rafka salati, sannan tace yannan badai angurya ba? Cikin tsoro ummi Tace, ni ma ban sani ba ko shine. Salati tsohuwa ne ta jawo hankalin umma tazo dakin da sauri. Tsohuwa Tace ina ga yarinyar nan angurya ne a gabanta. Umma Tace shine don wauta daga ke har abban kukayi shiru,

dubi tsawon watanin da kuka dauka, tsohuwa Tace yanzun yaya za'ayi umma tace ni ina nasan yanda za'ayi, ai ni na zata yanzun babu masu irin wannan ciwon. Rabon da inji labarinshi tun muna yan mata. Tsohuwa Tace kai nima na jima banji ba, amman kinsan dama wanzamai ke aikin.
Alhaji ya dawo daga sallar isha'i yaga abba tsaye a waje, Yace a'a babana dama baku tafi ba, Abba yace eh yanzun zamu wuce, ya biyo bayan Alhaji suka shigo suka riski zancen dasu dasu umma keyi. Alhaji Yace lafiya? Umma Tace yaran nan ashe zaune suka da lalura, tame inji Alhaji, umma Tace angurya ce ashe ta fito ma Ummi wai suka zaune. Alhaji yace meye kuma angurya Tace wani abu ne dake toshe mace. Nan fa suka shiga tattauna yanda za'a shawo kan abin, tsohuwa Tace wanzami za a kira ya yanka mata. Alhaji yace to gobe zai kira wanzami. ZURFIN CIKI book 4 part 25
ZURFIN CIKI book 4 part 25
Posted by Bashir Sani Fesan on 15 Dec 2016 - 14:26
Abba da jin haka sai ya fito, kishi fal da zuciyarshi, ya ce umma wanzami kuma? Ta ce eh, aikin sune. Yace gsky umma ba za a kai ta gurin wani wanzami ba , bagara muje asibiti ba. Tsohuwa ta ce, kaci gdanku da asibiti komai ku ce asibiti to wannan ba aikinsu ba ne. Abba ya ce, Nifa gsky ba xa a kai min mata gurin wani wanzami ba, umma asibiti zamu. Yanzu kai ya waye wanzamai ba duka suke dafa kayan aikinsu ba, haka kawai taje ta hadu da wata cutar? Alhaji yayi murmushi yasan kishi ne ke damun Abba, ya ce Babana kada ka damu, goben sai kuje asibitin, in sun ce ba su san shi ba to sai a zo a yi na wanzam ko ? Kunya ta kama Abba, Sam ya manta Alhaji yana gurin ya ce to Tsohuwa ta ce kuje in kun je ma dawowa za Ku yi dan me taurin kan tsiya. Abba ya ce naji kin ji ummi taso muje gda Tsohuwa ta ce oho dai, kuyi ta tafiya in dai akayi mata aikin ai dole ka barta ta warke . Alhaji da umma dai dariya sukayi ta yi musu, shi kuma yayi musu sallama, ummi kam kasa magana tayi don duk ta tsorata. Suna fita ta rike hannun Abba gam tana cewa. Don Allah ya Abba kada kabari

wanzam yayi mini aikin nan, zan ji zafi. Ya rungumota, Ba zan amince ba wani ya ganmin al'aurar mata, likita ma mace zan nema ko nawa zan kashe . Ummi ta ce, to zan ji zafi ya Abba? Ya ce, made ki damu, in asibiti ne kila suyi miki allurar kashe zafi amma in wanzami ne ina za ya ga wata allura yayi mini. Ummi sarkin tsoro ranar kwana tayi cikin damuwa, washegari kuwa tun bakwai suna asibiti. Babban asibiti suka je sun yanki kati likita me kula da fannin mata aka tura su. Mata dayawa suna ta kallon su ummi musamman yanda Abba ke nan-nan da ita, sannan wasu sungane shi kasan cewar shi dan jarida mai farin mini. Wasu mazan kuwa sai zuwa suke suna gaida shi. An kirata dakin ganin likitan, ta mike zata Shiga Abba shima ya mike, wata Nurse ta ce, malam jira mana, ya ce ai duk Mu biyu ne bamu da Ify, ya shige likitan namiji ne ba yanda ya iya dole ya yi masa bayani likitan yayi ma ummi tambayoyi in da duk ta bashi amsa/ ZURFIN CIKI book 4 part 26

ZURFIN CIKI book 4 part 26

Posted by Bashir Sani Fesan on 15 Dec 2016 - 14:27

Sannan ya bukaci ta kwanta kan gado ya saka safar hannu, juya kai abba yayi don gaskia ranshi ya baci, lallai ya kamata mata musulmai su dage suyi karatun likitanci don su taimaki yan uwansu mata. Sai da likita ya gama dubata sannan ya iya dubansa, likita yayi wani rubutu ya mika abba tare da cewa, an baku gado zayi mata aiki gobe ko jibi. Abba yace likita zan iya sanin wane ciwo ne wannan? Likita yace tsirone dake fitoma mata dai daiku. Sam abba bai fahimta ba don haka yayi mashi sallama. Umma ce a wurin ummi tana shan magani kafin ranar aiki inda abba hankalinshi ya rabu biyu rabi gurin aiki rabi garin ummi. Don ma umma ta koreshi da so yayi ya rika kwana, addu'a kam yana yinta. Ranar da za'ayi aiki abba hankalinshi duk tashe. Yana zaune bakin gadon da take kwance ita kuma tana can ana aikin. Wayar umma ce a hannunshi yana ta danne danne, ba don nishadi ba don kawai ya rasa me zaiyi. Dript ya shiga yana ta bin abinda ke ciki, mamaki ya cikashi lokacin da yaga irin

text din da ummi tasha rubuta mashi don ta tura ma abba, sai kuma ta fasa. Tamkar cikin mafarki abba ya rika karanta sakwanin dama ummi tana sonshi zurfin ciki ne tayi? Ya sake bude wani rubutu cewa, Ya Abba ina sonka, ina kaunarka duk wani motsi na numfashina kara sonka nake, ka tausaya mun sonka zai zama ajalina, duk ciwon da nakeyi na sonka ne. Ko na rantse ba zanyi kaffara ba, in kaji haushin kalamaina ka yafeni, nasan ni ba ajinka bace, amman ka daure kace kana sona koda bada gaske bane. Gama karanta sakon yayi dai dai da dawowa da ummi dakin, da sauri suka nufeta idonta biyu saidai daga gani tasha azaba. Tayi wujiga wujiga. Abba ya kama hannunta cikin matsanancin sonta da tausayi. Sannu suka dinga yimata, nurse tabasu magungunan da za'a rika bata, umma kuma ta dauki wayarta don sanar da alhaji an gama aikin. Abba yasa bakinshi dai dai kunnenta yace ina sonki ummi, ina matukar sonki. Duk da tana cikin wani hali taji kalaman nasa har a tafin kafarta. Ta bude jajayen idonta ta dubeshi, ya sakale hannunshi cikin tafin hannunta ya hade su. Ta girgiza kai dai dai lokacin da nurse din ta sake shigowa tace ga kayanta, ya amsa zaninta ne da siket da sauransu. Tace ka barta tayi bacci kafin ta tashi zafin gurin ya ragu, kila zuwa dare a sallame ku. Umma tace to mungode. Nurse tace yarinyarki nada dauriya, anyi mata allurar kashe zafi bata kama jikinta ba amman bata yimuna ihu ba. Likita ma ya yabata da kokarie ta, Abba ya kalli ummi cikin tausayi. Sai gurin karfe ukku ta farka wurin kam ya dan lafa da radadin, abba ne yaje gida ya dafo masu abinci sannan ya nufi wurin aikin shi. Don ranar bada wuri zashi ba. Tunda ummi ta farka take ta kokarie tunowa shin kalaman da taji cikin mafarki ne ko kuwa ido biyu ne? Bakwai na dare likita ya shigo ya kara duba ummi sannan yace suna iya tafia gida. Ya basu maganin sha sannan yace ta rika shiga ruwan zafi da dettol. Umma ta kira abba ta fada masu batun sallama. Yace su jirashi yana zuwa. Ummi tace da ummansu su alhaji pha? Tace sunxo kina

ZURFIN CIKI book 4 part 28
Posted by Bashir Sani Fesan on 15 Dec 2016 - 14:30
Bansan lokacin dana dauka ina rigimniya da sonki danqare a zuciyata.Ummi da ban sameki ba da tuni bana garin Kano domin lokacin yanke shawara nayi in nemi canjin aiki zuwa wata jihar har yau ban daina yiwa Salisu addua ba wanda shine mutum na farko da ya soma tsegunta min kin zama mata gareni So, Ummi baya raina abinda yake so da nayi zaton zubar da kima ne in furta maki kalmar so musammam in na tuna ke baki soma, zurfin a so bashida wani amfani don na sha wahala.Ba zan Qara boye dimbin son da nike maki ba Ummi ko gaban wa zan nuna kina jina matsala? Ummi wadda ke zaton mafarki take sai taji bakinta yana furta wayyo dadi Ya Allah kada ka farkar dani in har bacci nike Abba yace ciji yatsanki zakiji zafi Ummi nine Abban ki mai sonki wanda ya reneki tun kina zanen gobe. Hawaye suka soma zubo mata cikin muryar kuka tace Ya Abba da gaske kana sona? Nafi zaton tausayina yasa ka furta haka, Amma koba gaske ba ne na gode kuma naji dadi Amma ka sani Ya Abba ina sonka mai tsanani sai tasa kuka. Yace ummi yi shiru, in kukan takaici ne kukan ya kare. Nima na jima ina sonki jiya naga sakonki a wayar umma da kike rubutawa mai dauke da nuna sonki gareni. Sai zurfin ciki ya hanaki, don allah ummi kada ki koma zurfin ciki a sona, ki zazzage min duk irin sonki gareni. Ummi tace yau kam ji nake kamar a mafarki. Sun nutsa a cikin hirar so suna ta baiwa juna labarin halin da suke shiga a baya, a lokacin daya ganta da wani namiji yace hankalinsa yayi mugun tashi. Sai lokacin daya fuskanci bashir na sonta, ita kuma Tace ta tsani koh mace ta kira layin shi, zainab kuwa data samu labarin ta kamar ta mutu. Tace ko bishira bata kishi kamar yarda take kishin zainab, sunyi nisa basu san sun kwana zance ba, sai da ummi taji kiran sallah. Tace ya abba kaji abunda naji, yace sallah ake kira naji, kin sani kwana zance. Ban gaji dajin muryarki ba amarya tah. Ummi

tace gari yayi saurin wayewa kaje kayi muna godia ga allah ta hanyar nafita, yace to matata. Hamdala ta rikayi har bacci ya dauketa, muryar umma taji tana cewa ummi ki tashi kiyi wanka ki gasa jikinki. Tana zaune cikin baho wanda umma ta zuba ruwan dimi da dettol, tsohuwa ta shigo cikin bandakin. Ummi tace don allah tsohuwa fita, tace don allah ja can anki a fita din, ta saka hannu cikin ruwan wankan ummi dake gefe a bokiti. Tace ina suwaiba? Ai karo mata ruwan zafi, wannan ruwa yaushe zata gasa jikinta, idan da dan tawul dauko in danna mata jikin. Ummi tace nidai tsohuwa ki barshi don allah, sai kace wata mai jego? Tsohuwa tace tafi can kuda baku san darajar jikinku ba. Wannan rawar kan da mai sunan malam keyi idan ba'a gyara kiba saiki ba sai zance ya dawo baya, idan anyi magana ku yan zamani kuce bamu waye ba. Alhali ku wayewarku itace kwalliya amman jiki ba'a san a gyara ba, umma tazo ta kara mata ruwan zafi a cikin bokiti. Tsohuwa tace yau a sawo bagaruwa a tafasa ruwan shigar tata da ita don tayi saurin warkewa. Kuma ko ina zai hade, in kin koma gidanki kin kwana biyu ki dinga hada bagaruwa da alim kina tafasa su kina shiga.IKI novels / ZURFIN CIKI book 4 part 29

ZURFIN CIKI book 4 part 29

Posted by Bashir Sani Fesan on 15 Dec 2016 - 14:31

Umma Tace xa'asiyo tafita tabar su ummi nacewa to tsohowa kije mana tace bantafiya sai naga yanda xakiyi ganin ummi tabata lokaci nan tsohuwa ta dauki tawul din tashiga nadar ruwa tana dannama Ummi, Ummi tanacewa itadai abata tayi da kanta. Tsohuwa tace gaddamace daku ya'yan yau kinga duk macce dake rufe jikinta tafita daban damasu tallar jiki. Ita macce anfison a sameta ko yaushe da dumi a jikinta, yawo babu takalmi ko a tsakargidane yana ragewa mace dumi sbd sanyinda ke ratsa tafin kafarta har ni'ima yana ragemata. Sannan zama atantagaryar suminti shima yana rage mace, da a ace zaku gane kunga masu saka hijabinnan da safa? bakaramin wayo suke yimukuba. Inda za'a banbance za a samu sunfiku ni'ima da kyau fata,

don haka sai kin dage Ummi dai tayi shiru, amma aranta cewa take wannan tsohowa ko ina tasan wannan duk bayanin? Filo aka ajewa Ummi ta zauna tana karin kumallo, duk takosa taga abbanta, koda ta tsinkayi sallamarsa tamkar tamike ta taroshi. Amma dole yaje yagaida su alhaji, tsohuwa tace aefa mu kuma bana munga takanmu don nan zaka dinga likemana. Yace dadin abundai nima nan gidan ubanane, da uwata. Umma tana kicin tanamasu dariya. Tunda ya zama idanunsu sunsarke da juna sun kasa ko magana Ummi ce tayi karfin halin lumshe ido sannan tabude tace sannu daxuwa. Tasowa yayi ya tsugunna kusa da 'its, yajikin babyna?sunan yamata dadi, naji sauki bari in kawomaka abun karinka. yamika mata tafin hannunsa tasaka nata yahadasu ya yasarke, murya kasa kasa yace barshi na' amso. Ta kula abba mutum ne maison wasa da tafin hannu. Ita kanta tanason hakan da akwai wani sako da tafin hannu ke isarwa acikin duniyar ma'abota so, kila wannan dalilin ne yasa abba ke kashema tafin hannusa kudi da mayukan da ke saka laushin hannu har ita mah ya saimata. Koda umma ta shigo Ummi tayi kokarie amshe hannunta amman abba yaki saki, kuma a hakan ya karya. Umma kasa zaman dakin tayi domin a baki abba yake ba Ummi abinci, umma nafita taceels / ZURFIN CIKI book 4 part 30
ZURFIN CIKI book 4 part 30
Posted by Bashir Sani Fesan on 15 Dec 2016 - 14:33
Daren ranar duk suna kan kujera doguwa a dakin umma ya bude mata laptop wai yana koya mata kanta kwance a cinyarsa, umma ta shigo dakin tsohuwa tace tsohuwa zaifi kyau mu sallami yaran nan na gaji da ganin wannan aiki nasu ai tasamu sauki. Tsohuwa tace suwaiba ina laifin ta kwan goma ma, umma tace anya zasu kwan goma nan? Gobe bakwai guda ta koma dakin ta, tsohuwa tace shine nan. Abba yace Ummi kinfa samu sauki ba zakizo mu koma gidan mu ba? Tace su umma ne zasu maidani ai nima ya abba inason in koma yace yau nan zan kwana in sunga haka sun kuramu, Ummi tace ya abba kayi hnkr

kada ka kwana, shine yace kin yarda goma inxo mutafi ko ba sanin su umma? Tasa dariya tace taf inajin kunya bazan iya binka ba yace to kuwa zan kwana a nan. Suna cikin haka umma ta leko tace abba bazakaje gida ba yanxo fa sha biyu saura, yace umma nima nan zan kwana. Ta rike haba nan din lafia? Yace to umma nima ba gidan mu bane? Ummi tace dama yafi umma kada yaje wani abu ya rudashi, umma tace a'a abba tashi ka tafi insha allah gobe Ummi zata koma yayi murmushi tare da cewa nagode umma.nan dai ya tattara yanashi yanashi ya tafi gida cike da kewar matarshi, itama Ummi lamo tayi a gado. Bayan umma ta gama yimata fada ta bari ta warke taki ko, sai cewa tayi umma ni fa na warke. Umma ta kalli Ummi cike da mamaki tace yaran yazo saidai a barsu. Shiyasa akace idan macce ta isa aure ayi mata a huta. Ita kam Ummi tana ganin a barta tabi mijinta ta faranta mashi shine abinda yafi dacewa don yanxu ba inda ya kai mata dakinta dadi bacci. Duk da kashedin da tsohuwa tasa abba dakinta tayi mashi na cewa ya bar Ummi sai ta kara sati kafin yace zai kulata da sunan auratayya, bai sa abba jin zai iya ba. Don haka koda ta fada mashi cewa yayi kadai da huruminki da wanda ba naki ba duk sai kin shiga? To nidai ki lafa man haka. Ya fice a dakin. Ita kuma tana ta fadanta tana cewa "Na shiga din dan neman yaro, da kyar ya barta ta kara kwana biyu ya afka mata don shi hkr sa ya kare, ta nuna mashi ita fa tsoro take ji kada ta wahala, ya lallasheta yace ba wani wahala. Ummi tana son faranta ran mijinta. Don haka ta jure duk da yarda yazo mata ba sauki, sai dai tasha albarka kuma ta kara samun wani matsayi na musammam a gunsa. Cikin satin ta zama yar lelenshin kafin sati biyu ta hardace duk wani darasi da abba yake koya mata, abba jinsa yake kamar wannan lokacin ne ya fara rayuwar angoncinsa. Sam ya manta yana da wata mata uwa duniya saida Aunty ta kirashi tace lafia baya kiran matarsa sai ga abba da girman shi ya girba karya. Wai ya kira ya kasa samunsu Aunty ta

yanda tunda farkon tafiyarsu yana kiransu sun gaisa da bishira tana tmbyrshi ina hibbarta? Sai lokacin ya tuna kwana biyu bai ganta don tana gidansu umman bashir, amman sai yace tana lafia in yaje zai kirata taji gwarancin yar tata. La'asar sur suka jero ita da abba don su dan zaga kurum. Sun shigo gidan ahmad da muktar duk basu rabu ba saida sukaji sun saba da ummi. Don ita haka take yana da wuya kayi zaman awa guda da ita bakaji ta kwanta maka a rai ba. Abba yaji dadi yarda Ummi ta nuna kauna ga matan abokanin nasa, yasan bada jimawa ba matansu zasu zama kawaye kamar yarda yaso da bishira amman taki. Daga can suka nufi layin su gidan su umman bashir Ummi tace su fara shiga su dauki muhibba abba yace bazata yarda dake ba. Ummi tace zata yarda muje a ran abba tsoro yake gada umman bashir ta gwasaleta Ummi, sun sameta tana shara da sauri Ummi ta amsa ta soma sharewa hakan ya faranta ran abba sai dai da ya kalli umman bashir yaga tana hararar Ummi, saida ta gama taxo ta zauna suka gaisa abba na rike da hibba tayi kaca kaca da kunu gashi duk ya dunkule dama ko lokacin da bishira tana nan haka zakaga yar duk kazanta. Ummi ta bude post dinta ta cire dari biyu guda biyu ta mikawa umman bashir gashi umma kin sai goro saida ta tabe baki ta amsa babu ko godia, sai dai abba cikin jin dadi yace angode, da hibba taki binsu Ummi tace kamal xo ka siyo wa hibba alawa, kinga baba kamal baya nan xo muje in sayo maki. Cikin sa'a sai taxo zasu fita sai ga bashir dauke kai yayi tare da jan tsaki daya shiga gidan sai ya hau umma da fada Wai ta daina barin Ummi da wannan abba suna zuwa in ba haka ba zasu kawo mata wani asiri. Umman bashir tace suta zuwa ma indan ta nine mi jiya tayi bare yau, ka gansu dari hudu yanxu ta bani don haka bazan hana zuwa ba amma fa ina nan yarda nake bazan canza ba, suna shiga gidan su umma kicin ta wuce ruwan zafi ta zubu ta cude muhibba tas, ta wanke mata kai ta chajeshi ta shafeta da mai nan ma basu jima ba suka nufi

gida zanen umma ta ansa ta goye muhibba, shine ya bude dakin bishira duk kayan yarinyar sun rine da datti, Ummi dai ta zazzaba yace .ba maidata za'ayi ba, Ummi tace ta dan kwana biyu mana. Yace tana fitsari fa. Ummi tace kasawo muna pampers Yace shikenan duk da ya nuna bayaso yarinyar ta zauna gurinsu amman yaji dadi sai lokacin bacci daya shigo ya shigo da pampers din ta saka mata Sannan ta kwantar da ita can gefe ta azama mata pillo guda haba guda baya, su kuma suka kwanta a nasu makwancin suka cigaba da soyewa. novels / ZURFIN CIKI book 4 part 31

ZURFIN CIKI book 4 part 31

Posted by Bashir Sani Fesan on 15 Dec 2016 - 14:36

Ummi tana son yara don haka hibba ta dinga samun gata, satinta guda umman bashir ta dinga jaraba sai an dawo da ita. Wai kwadayi ne don in bishira tadawo ta bata tsaraba, amma koda ta tafi da hibban yarinyar sai taqi sai kuka har dasu amai. Dole aka dawo da ita, don alhaji karami cewa yayi atattara mata kayanta duka inyasake samun an maido da ita sai ya saba ma umman bashir. Hakan da babbar sallah abba yakashe musu kudi ita da hibba, sai dai duk abinda yasai ma ummi to ya aje ma bishira nata. Ita kam tana can duk addu'arta akan ummi ne, kafin ta dawo ummi tafita, don haka data dawo da kwarin gwuiwarta ce wa bazata samu ummi agidan ba. La'asar sakaliya, direban gidansu ya iso da ita gidan kamar yanda mahaifinsu ya umarce shi cewa in ya dauko su kada yaso dasunan, ya dire kowa agidanta. Kasancewar unguwa uku suka soma zuwa sai anty ta taya bishira diban kaya su shiga. Daidai kofar dakin bishiran abba na kwance rigingine, 'yar T-shirt ajikinshi fara kar. Dawandon jeans gajere iyaka gwuiwa. Ummi kuma dogon wando ne irin mai kama jikin nan dariga mai kamar singileti kanta yasha kana nan kitso, tayi filo da kirjinshi yana bata labarin wata mota da yake son yabada tashi yayi ciko. Ita kuma tana ce masa ya dai je ya shawarci umma, muhibba kuwa tana ta faman wasa da sabbin kayan wasanta da ummi tasai mata. Ita ma cikin

'yar shimi mai kyau, kanta kuwa ummi tayi mata kitson (3 in 1). Sororo bishira ta tsaya tana kallonsu, sam bata tsammaci a irin addu'ar datayi zata dawo ta samu ummi agidan ba. Basu ganta ba saida anty tayi sallama tare da cewa, ya naga kin tsaya? da sauri suka waiwayo duk suka mike. Gaban ummi yayi wata muguwar faduwa, amma duk dahaka cikin fara'a ta nufe su, bishira ta hade rai matuqa sannan taqi ko kallon ummi ta nufi 'yarta. Anty kam cikin fara'a suka gaisa da ummi harta zage jakarta dake kafadarta tabawa ummi wani dan agogo mai kyau. Nan dai ummi tayi ta godiya shima abba ya mata godiya. Abban ne ya shigar mata da kayan daki, ummi tana cewa anty kin mana dawowar bazata, dakin fada da an share miki dakin. Nan ma bata tanka ba, ummi dai data gaji dayi mata sannu bata amsa ba sai kurum ta nufi dakinta, zuciyarta babu dadi, tasan yanzun ya Abba zai raba jin da yake da ita zuwa su biyu. Bishira tayi kyam tana ta qamshi don anty baza su barta tazauna masu da qazanta ba, ga haqorin makka an sako ana ta qwambo. Ranar dakinta Abba yakwana, yanda bata ga wata rawar jiki daga gare shi ba tayi zargin ummi tasamu lafiya. Hakan ya qara dagula mata lissafi, tayi rabon tsarabarta daga kawayenta sai maqota, don ko umman bashir daga zam-zam bata qara mata komai ba. Dama tana cike da haushin umman data bari ummi ta daukar mata 'ya gashi nan muhibba ta liqe ma ummi. Hakan ya shaqar da umman bashir har tace amaida mata zam-zam dinta ita bata sha. Wato don taje makka shine zato zo ta canza hali? Ita kuma bishira ta amsa tare da cewa, ai ba ita ta aike ni makkan bada har sai tazabi abinda zan bata. Ummi ko zam zam din ba abata ba, kuma ko ajikinta. Abba kam shita kawo masa dogayen riguna da T-shirt masu kyau, amma su anty ne suka matsa mata sai ta saya. Ranar daya dawo daga dakin bishira ummi tana fashin sallah gashi yanuna yana dalarura alokacin. Sai tace ta yafe masa yau dagobe yaje gurin anty bishira, yace A'a tace ba haramun bane nina amince, yace

nasani. Shiba yason sai yatafi tafara damuwa ko tazo tana jin haushinsa, tace ba komai saida yatafin kuwa har kuka tayi don kishi. Amma tabawa zuciyarta hakuri tasan wata rana wannan jarumtar datayi zata zame mata alkhairi. Ita ko bishira koda yazo mata sam bata damu ta bincika ba, tunda taga ba girkinta ba, saima ta hau murna yayo satar kwana ya bata musamman dataga dayayi wanka yakoma dakin ummi, haka washegari. Don haka sai tashiga daga hanci har da 'yan habaice habaice, kafin tadawo tun da dama da namiji dan uwansa yake kwana. Tana nufin ummi bata ba tayi masa amfanin komai wannan yasa ummi ta daura aniyar cusa mata takaici, aranta tace tunda cinikinki labe nikuma zansa miki hawan jini. Kamal yazo daukar abincin da ummi ta saba sawa yau har da kunun gyada tayi. Bishira ta kalle shi, wai kai wannan abincin na waye kullum kake zuwa dauka? Yace na ummarmu ne. Ta taba baki, ummar nan taku kwadayinta yayi yawa, ko kuwa itama asirin ya kamata ne? Kamal kuwa yaje yafada sai ga umman bashir agidan suna zage zage da bishira, tana ce ma bishira dadin abin gidan dana nazo kwadayin ba gidan ubanki ba. Marowaciyar bnza ai dama ina da cikinki, lokacin da Abba yasai maku TV, yace ki bani naki sai ki kace gara kiyar. Bishira tace, Eh na hana TV aiba wani shegen ya sai minba, ubana yasai min, kuma nace mai kwadayin yarinyar daki kace uwarta mai asiri, menene na amsar abincinta kici banda kwadayi? Shiyasa kika bata 'yata ashe don asami abinci ne, umman tasa kuka ni ke ke zagi? Yau ko abba zai zo gidan nan zai zaba ko ni ko ke. Ummi dai tana daki tana jinsu. (aranta tace dadi na da gobe saurin zuwa). Bishira tace dama ya darajaki ne shine za kice haka, yazo din nace mai kwadayi harda rainawa na baki zam zam butulu duk abinda na miki kin manta kece kika aikeni makkan? Umman tace, zuwa makkan naki dashi gara babu, don nasan da kyar ne in za akarbi wannan aikin nani ke da bakya sallah arniyar banza qazama. Ummi harda riqe ciki don dariya,

haka dai suka yi tayi wajuna gori har dai 'yan kallon da suka taru suka soma bda haquri, umman bashir tayi gida cikin kuka. Tagayawa 'ya'yanta komai su bashir dasunce sai sunje sun zaneta umman bashir din tace barta ku barta kawai bari abban yadawo. Da dare ta ritsa shi agidan yasha mamakin wai yau mahaifiyarshi da bishira ne suke fada yace hakane dama duk zamantakewar da ba'a kafata don Allha ba wata rana sai ta rushe. Nan yayi tawa bishira fada da cewa uwarshi sa'arta ce dazata tsaya ta dinga gaya mata magana? Nan fa aka sake kacamewa har abba. Yakai ga kwasa wa bishira mari, sakamakon irin rashin kunyar data rike qugu take tsulawa umman bashir din. Ummi ganin abin yana tsawo ta fita taja umman bashir tana bata haquri ta zaci zata hantare ta amma sai taji tana cewa ba komai ummi sakayya ce tunda na nuna ina sonta dole tamin haka. Abba yace ummi tasa mayafi taraka umma gida, hakan ya qara qona ran bishira gashi yanda taga Abba ya bata rai zai iya yin komai, dole ta koma daki tana cizon yatsa tare da tunanin mafita. Ummi kuwa ahanya sai lallashin umman take tare dayi mata alqawarin cewa duk abinda take so ta tambayeta zata mata shi tarakata har gida sannan tadawo. Sabon kuka umman bashir tazauna tanayi, takaicinta yanda bishira ta zage ta taci mata mutunci agaban ummi, tashare ido tare dayin ajiyar zuciya a fili tace dani take magana. Ynzun ummi tasan kishi fiye da baya, don ta hau turbar ma'aurata kuma tasan muhimmancin abinda ake yiwa kishi, don haka zatayi komai na jan hankali don ganin taja mijinta gareta. Kuma inta lura cewa bishira ta maqale mata aqofar daki sai tayi ta jan abba da wasanni, don ta quntata ma me labe. Amma hakan baisa ta daina ba, don haka ta daura aniyai saita mata abinda zata tona kanta ha abba yasani. Duk jumma'a abba yana dawowa gida musamman in ranar girkin ummi ne don cin abinci na musamman. Jumma'a biyu kenan bata fado kanta ba sai wannan, don haka tun alhamis taje ta yarfo kitsonta, ta biyo ta gidan su gurin

tsohuwa tazo. Don haka suna gaisawa da umma tace gurin tsohuwa nazo. Suka shige daki tace da tsohuwa nazo ne indan samu dan wani sirrin. Tsohuwa tace, name ummi? Ta ce na gyaran jiki mana. Fati tace min kwanaki kin fada mata wasu abubuwa. Tsohuwa ta ce, ja'ira, kinga uwar bari? Dama nace zaki same ni ina kyakkyawan zamana, bada ina fada miki kina sharewa ba? Ummi tace haba tsohuwa banaso aji mu yanzun dai ki bani shawara sannan ki fada min abinda zanyi inja hankalin mijina. Ta ce, toda farko ki dinga kula da jikinki ta hanyar rufe shi ruf, kada kibar kofar iska. Banda tafiya ba takalmi, iska tana shiga tanan kuma mace narage ni'ima banda zama ba dankwali inso samu ne hatta tsarki ki daina yi da ruwan sanyi, ki dinga yida ruwan dumi. Sannan ki amshi bagaruwa gurin ummarki ki dinga shiga inkin tafasa da alif dakuma saiwar mata, sannan inkinyi al'ada kin gama kinyi wanka toki dinga matsa farin miski a ehem dinki. Sannan ki samu saiwar kankana, saiwar zogale, kanunfari, mazarkwaila dazuma amma kisa kanunfari dayawa sai ki dafa su su dafu kullum kisha kofi biyu safe da yamma. Sannan ki aya garinta, kwakwa ma kiyi garinta, dabino ma kiyi garinsa, sai ki dinga diban cokali bibbiyu ki zuba amadarar ruwa sannan ki zuba zumarki mai kyau kisha, sai ki samu kuma gwanda, kankana, abarba, zogale, citta, lemun tsami, ki markada su kisha. In anan maki katsaya yarinya zakiji ki kin cika cindum daruwan ni'ima sai kin samu martaba ta musamman agurin miji dan zaijiki kin fita daban da dukkan sauran mata. Ki hada da biyayya tsafta da kuma iya tsara girki mai dadi. Ummi tace, toni yanzun yaya zanyi nasamu saiwoyin nan? Tace, bari zanba matar ado dake yawan zuwa kasuwar qauye zata zo miki dasu. Amma su gwanda gasu nan bakin titi ko shi sai kice ya siyo miki, zogale kuwa baki rasa shi gurin ummarki, har da cittar da alif din da bagaruwan. Ta ce to, ta tafi gurin umma ta amsa har taje gida bata daina mamakin tsohuwa ba, ya akayi tasan duk wadannan hadin matan? Amma data

tuna cewa 'yar katsina ce sai tace ba mamaki. Tun ranar alhamis din ta soma aiwatar da darussan da ta debo daga tsohuwa, safiyar jumma'a ranar zai bar dakin bishira. Ya fito tana sharar tsakar gida ta gaidashi, ya amsa da fara'a, tare dawani kallo mai fassarar in ba keba. Cikin muryar data adana don shi kadai tace, ya abba ina son in je ayi min zanen fulawa. Yace jiya kin fita yau kam a'a. amma ki aika akira mai zanen tazo ta miki. Ta marairaice, towa zan aika yaya abba? Yace aike ni, ina ne gidan? Tace layin su umma ne yace to za'azo ai miki. Bishira tafito daga daki tazabgga ma ummi harara, Tare dacewa kisisina. Abba yakalleta, kema sai tayi miki. Tace bana bukata, aikin banza, shikam yafice. Ummi kuwa tace gaba da aikinta, ita ko sai tasa kujera tazauna tana sakin zantuka, eh don kwalliyar tabanzanta tunda ba a iya biyawa miji bukata. Allah dai yasa ya fada min komai, to ni me zai dame ni don 'yar aiki kawai na dauki yarinya. Tashare min gida, tayi wa mijina abinci, daga nan fa? Saita saki shewa, ummi ta ce aranta yau zan bambance miki. Birabiskon shinkafa tayi da miya, ta wadata birabiskon da kayan lambu, miyar ta dauki nama da bushasshen kifi. Sannan ta hada musu kunun aya yaji dabino da madara, ta aikawa ummanta lokacin da kamal yazo daukar na ummarsu. Tasheka wanka taci doguwar rigar shadda koriya mai duhu, ta kafe dauri tamkar yau ne daurin aurensu. Ga fulawar da yaje ya biya akazo aka zana mata. Tanajin rigimar muhibba tafito tazuba mata adan kwano tazaunar da ita akofar falon mamanta.bishira tafito kicin baki tasaki tana kallon ummi da tazo wucewa harda bangazar ummi, nan ko kamshi ya bude ta na turarukan da ummi ta fesa. Abba yana yin sallama ummi tafito da sauri, oyoyo yayana, bishira tana daga kicin dinta tana kallon su. Ummi ta rungume shi, sannu dazuwa sahibina. Ta amshi ledar hannunshi dajakar, yace yauwa sannu babyna tace inazan kai ledar? Yace akwai ta bishira aciki ki ciro. Ta mika mishi ledar ta wuce dajakar dakinta. Ya mika wa bishira lemo

da abarba da yayo musu tsaraba sannan ya wuce danasu, awulakance ta aje. Yana shiga ummi tadan karo kofar yanda bishiran zata iya lekensu sosai ta gefen kofan. Ta cire masa hula ta aje akan madubi sannan ta kunna fanka. Ta shirya masa abinci, yauni zan baka har ka qoshi. Haka suka yita baiwa juna abaki har suka qoshi. Yakamo hannunta mai qunshi yana ta sumbata, wai kamar kada su goge. Kumatun shi ta shafa nima yau kamin kyau, koda yake dama kai me kyaune, ina sonka ya abba sosai. Cikin jin dadi ya mannota a jikinshi, nima ina sonki, ina manta kowa da komai in muna tare, tace ina tsoron kada wata rana ka juya min baya. Ya saqalo hunnuwansa cikin nata ina fata in mutu kafin lokacin. Ummi tasomayi masa wasu irin darussa wadanda tasan yana saurin tada sha'awarshi nanda nan kuwa tasa shi fita hayyacinsa yakama surutai. Ummi ta tabbata bishira tana wurin ta labe, don haka tai murmushi ta bishi suka tafi duniyar ma'aurata. Bishira tamkar tayi hauka sai kawai ta fado dakin tana fadin, maciya amana, har yanzun ba afita daga lokacin girkina ba munafiki. Abba ya tashi sannan yaja riga yasaka, ok dama kina labewa ne kiji sirrinmu? Da taga ya sauko da zafin rai saita gudu dakinta. Yabita yamata tatas, kuma ya fada mata cewa tazo ta shiga dakin ta zauna ba labe ba, yanzun zai komane yaci gaba daga inda ya tsaya. Tayi ta kuka gashi ba damar zuwa gurin umman bashir dole ta tafi gidansu. Shi kam abba shareta ya yi kosu umma bai fadawa ba. Sabuwar soyayya ma ya balle agidan, su ci abinci tare, wanka tare, su fita yawonsu a qafa ko amota. In yana gurin aiki bini- bini ya kira waya, ita kuma ko yaushe cikin kirkirar girki da kwalliya tare da dadadan kalaman dazata fada masa take. Duk lokacin datayi masa zancen bishira sai ya ce, don Allah ta bar ta ta huta, ummanshi kuwa 'yar bin qwaqqwafi sai da tabi ta gano bishira bata nan. Don haka koda ya shiga gaisheta sai tace kada ya yarda yaje yama bata takardarta. Ita ko tana can uwarta tace ma mahaifinta abba sakinta yayi, shi kuma yace to

sai tazauna tunda zaman gidan take so. Amma su sani daga abinci sai ruwan gidanshi ya amince tayi amfani dasu sai ko gurin kwana, amma bnda wannan ko makilin dinshi ta taba bai yafe mata ba, wannan hukunci yayi musu tsauri. Ko wata bata rufa ba taji gidan ya isheta don hajiya zainu taso maidata makaranta amma yace tagama boko. Bishira na zaune ta zuba tagumi hajiya zainu ta shigo dakiki tace tagumin menene kuma? Tace, su sumayyah ne wai nace suyi ma muhibba wanka sukace Allah yakiyaye. Wai tunda nazo dakinsu ya lalace da kazanta, hajiya zainu tace aiba karya suka yiba, don haka ma maida yarinyar nan za ayi ke kuma ki koma gidan antynku ko ki tafi abuja gidan aisha. Tace baxanje gidan aisha ba, don itama bama shiri, gara gidan antyn amma gsky ni abarmin 'yata kuma fakinsan bai sakeni ba. Tace, inda ubanki yasan ba saki bne da tuni bai kora kiba? Don haka mubarshi haka amma batun 'ya nice zan maidata. Ranar da ummi takira ummansu tafada mata cewa bishirafa tuntuni tayi yaji amma Abba yaqi zuwa, umma ta kira shi tace inya dawo gurin aiki tana son ganinshi. To kafin yadawo ma saiga hajiya zainu da direba tazo gidan su umma tadire musu 'yar, sannan tashiga gidan umman bashir tace, in kin haifi danki na halas ne ba shege ba to kisa shi ya aiko wa 'yata saki. Umman tace zoko kiga dan halas ne in yaso kuje ku nemi arne mara sallah dan uwanta kazami kubashi. Nan fa zage-zage ya tashi har su umma dasauran makota suka shigo. Dakyar aka tura hajiya ta tafi, tace kuma saita kira 'yan sanda anzo antafi da umman bashir. Alhji qarami ma cewa yayi maza abba Abba yarubuta takarda ya aika ma bishira.ZURFIN CIKI book 4 part 32

## ZURFIN CIKI book 4 part 32

Posted by Bashir Sani Fesan on 15 Dec 2016 - 14:37

Shiko alhji babba da umma suka ce a'a abari qura ta lafa sannan aje. Koda aka kwana 2 abba kin bin alhaji yayi sai wani abokinshi alhaji yasamu suka tafi tare. Mahaifin bishira yaji mamaki cewa ba sakinta abba yayi ba. Kuma bai san sun maida 'ya ba, tadai ce mishi kunzo kun

amshi 'yarku, to yanzun tunda haka ne kunga kenan bishira da uwarta basa son takoma gidan mijinta ko? Su alhaji suka ce eh, yace to ku sa shi ya rubuto takardarta ku kawo min, su alhaji sukace ba za'ayi haka ba. Yace, to kuje ku barta zata gane gidan ubanta bananne yadace tazauna ba. Sukai godiya suka tafi. Harta koma gidan anty farida mahaifinsu yace tadawo nan gidanshi badashi take takama ba? Wato ta kashe auranta zata je ta kashe na yarta dole ta dawo, tsohuwar dake musu aiki yace ta koma gida tahuta amma duk wata tazo ta amshi albashinta. Sannan yace bishira itace zata dinga wannan aikin duka ita kadai, lamarin yayi wa bishira tsauri da yawa, gashi ba fita duk ta rame ta lalace ga tunanin 'yarta. Muhibba kuwa tana gurin umma, ummi ma takan daukota sannan ummi tasamu nasarar rufe bakin umman bashir, ta hanyar yi mata kyautuka ko me sukace sai ta aika mata. Tasa Abba ya canja mata gado don nata ya lallace, sannan da fati ta haihu tasa Abba ya sai mata garar abinci, ita kuma tasa zani da rigunan yara. Nan fa sai ga sahura babu ko kunya tana shima ummi albarka, ko bashir ne yakawo gulmarsu ummi sai tace ai ita bata yo halin uwarta ba. Tafi-tafi ma in ya kawo sai tace ai su umma da ummi sun gane kuransu. Haba sahura kodai ki gane kuranki? Abba yasoma damun ummi da batun ciki, wai shifa yana tsoro kada su gaji su umma, ummi tace su dai yi addu'a sunje asibiti ba wata matsala, likita yace in rabonsu yazo zasu haihu. Da kyar ummi ta shawo kan Abba ya amince ta zana (JAMB) don ci gaba da karatu, sannan ta shiga islamiya. Abba yayi kyau yayi kiba ya kara gogewa, haka nan ummi duk wanda yaganta saita birge shi, daka ganta kaga wayayya wadda mijinta yasan da ita. Taci nasarar samun (POLY) saboda bata samu abinda take so don zuwa (UNIVERSITY) ba, sai dai ba tasha dokoki kafin ta fara zuwa. Bayason kawaye baya son abokai, irin wanda wasu matan keyi sannan yadinka mata manyan hijabai, kuma banda hawa acaba, inya samu sarari zai dinga zuwa da kansa

yana daukarta. Sai kuma gargadi na karshe kuma da babbar murya, in har ya daina samun kular datake bashi ta kowane fanni wai saboda karatu, to kuwa za adaina karatun gaba daya. Tace, insha Allah sai abinda yai gaba. Ya canja mota, umma tayi ta fada wai tafi son yasai fili yayi dan gidanshi irin na zamani yace za'azo gurin ahankali kada ki damu umma. Bishira ta sulale ta tafi na'ibawa gidan anty da kukanta wiwi don Allah ta taimaka mata taba Abba hakuri ya maida ta, wlh tagane kuskurenta. Anty tace, nifa bazan iya kiran Abba ba don kin riga kin bmu kunya, sai dai in ke ce zaki kira shi ga waya can. Ta dauko ta kira, shikuma ganin kiran anty sai yayi parking yadauko ummi daga makaranta, ya daga sai yaji muryar bishira. Cikin kuka tana cewa, don Allah abba nice, kayi hakuri indawo dakina, wallh zan canza, yace ok baki riga kin canza din ba, to bari inkin canza din sai muyi magana. Yakashe haka tayi ta kuka tagama anty tabata wasu kayan sawanta sannan ta tafi. In lokacin labarai yayi haka take zuwa ta tasa TV tayi ta kallonshi tana kuka, kullum kara sonshi take gashi yayi kyau idanunshi sun qara haske. Wata ranar jumma'a wuraran karfe sha daya ta saci jiki tanufi gurin aikin Abba, yana fitowa dakin daukar labarai akace wata tana nemanshi. Baiji wani mamaki ba don mata kanzo neman shi wasu suce suna sonshi wasu suce ganinshi kurum zasuyi don yana birge su. Yana zuwa sai yaga bishira, nan take ya daure fuska tamkar bai taba dariya ba, duk da cewa acan kasan zuciyarshi yatausaya mata. Ta tsugunna gwuiwa 2 tana rokonsa, yace ke tashi kada ki janyo min mutane, jeki zanzo. Koda ta tafi cikin murna shi ko harkokinsa yakama. Shiru-shiru tana saka rai bashi ba alamarsa. Nan kuma tashiga daukar waya kannanta tana kiranshi, harma yadaina dagawa. Wataran taje tasamu ahmad tana kuka, ahmad yace taje zai ganshi. Rannan kuwa har gida ahmad yiyi sallama da abba yashiga rokon Abba ya maidota. Abba yace taje taroqi mahaifiyarsa dasu umma insun yarda shikenan. Har gida

ahmad yaje ya fada mata, bata yi sanyi ba tanufi gurin umman bashir. Umman tana zaune da 'ya'yanta suna shan farfesun kifin da ummi ta aiko musu dashi, tana ganin bishira ta hade rai. Tace, lapiya? Bishira tace lpy lau umma zuwa nayi in roqi gafararki. Tace nime kika min? Tace don Allah dai ki yafe ni, ina son indawo dakina Abba yace sai kin hakura, tace oho, yanzun kin yarda ina da kima agurinsa? To bari kiji bazaki dawo ba, mai baqar rowa kince nimai kwadayi ke kuma mai rowa ko? To kin gani wannan ummi ce ta dafo mana ta nuna mata kular kifi, sanda kinanan bana cin komai bansan dana yana samu ko baya samu ba. Yanzun abin arziki iri-iri kidawo ki toshemana kofar samu? Tace, wlh bazan toshe ba, umman bashir tace dukda haka dai bazaki dawo ba. Tayi takuka sannan tafita, har zata wuce gidan su ummanshi sai ta tuna kada suyi mata dariya sai tace baridai ta shiga. Kyakkyawar karba umma tayi mata suka gaisa, tazauna umma ta kawo mata ruwa ta amsa tasha. Muhibba tana ta tsalle tsallenta kan kujera zuwa jikin umma, umma tace ji hibba ki gaida mamanki, ga mamakin bishira sai yarinyar ta kalleta tace. Umma niba wannan bace ba momina, momina sun tafi da babana zaya kaita makaranta. Umma tace, wannan ma ummarki ce yarinyar taruga dakin tsohuwa tana cewa, ita ba ummarta bace. Bishira ta bita dakallo, yarinyar tayi bulbul gata cikin shiga mai kyau da tsafta kanta yaji kitso da 'yan duwatsu. Saita soma kuka tana fadin mahaifiyata ta cuce ni, umma tace a'a kece kika cuci kanki, inbaki dauki damuwarki kin kai mata ba yaushe zatasan anyi? To ynzun dai dubi 'yarki tana gudunki sbd bata sanki ba, ina amfanin wannan? Tsohuwa tace kukan wanikeji ta shigo tana kallon bishira cikin mamaki tace. 'yar nan kece haka? Ciwo kikayi ko ko duniya ce ta juya miki baya? Kai jama'a dubi yanda kika kare kikayi bikinkirin. Ita da tadukar dakai tare da cewa bnyi ciwo ba nidai nazo ku yafe ni, sannan ku roqa min abba ya yafe min in dawo dakina. Yace, bazan dawo ba har sai kun

yafe min, amma naje gurin umman bashir ta kore ni tace bazata bari in dawo ba. Kuma gidanmu wuya nake sha, kusan rabin aikin gidan nikeyi ga qannaina duk sun raina ni. Umma tace, yi shiru share hawayenki bari zaki koma. Tsohuwa tace, ke dai kin cika sa kai a uku suwaiba, gashi abin kirki bai karbe kiba. Kina yi ana zaginki ana zagin 'yarki, bishira ta ce wlh duk na daina, yanzu na gane kune masu sona, umma tace ba komai. Tadaga waya ta kira alhaji ta fada masa komai yace to yana zuwa donshi ya qosa asulhunta yarinyar ta koma dakinta saboda darajar tsohonta. Yana zuwa yaji komai nan ya daga waya yakira Abba, yace yana zuwa yana hanya ne yace to ya same su gida. Abba yana shigowa ganin bishira yahade rai ya zauna nan dai alhaji ya hada su yayi musu fada da nasiha, sannan yace baya son abba yace komai komai kuma ko sun koma gida banda tashin tashina. Bishira tayi ta godiya alhaji babba yace su tashi ashiga gurin umman bashir din tana ganinsu tahau cewa alhaji dakanka? Maimakon ace in zo? Umma tace, a'a keda zamu zo baki hakuri ai mu ya dace mu shigo. Nai dai alhaji yayi bata hakuri tace taci albarkacinta na hakura, amma da sharadi inta sake maimaita halin da tayi abaya ko taje ta takurawa ummi tofa saita tabar gidan. Bishira cikin kuka tace ta daina insha Allahu, nan itama umman bashir din tace dasu umma su yafe mata sharrin shaidan ne da qaryar barayin imani wato bokaye da 'yan tsibbu suka ce ba komai. Nan alhaji yace da abba yakai bishira gida, ba don son ranshi ba yadauke tazuwa gida, sam bata damu da daure fuskarshi ba, dadi da murna fal ranta. Yana sauke tazai wuce tace, don Allah ka yafe min sannan ka gaida min ummi, yace zataji. Tace to yaushe zan dawo? Yace, duk lokacin dasu alhaji suka zo gurin dadynku. Nan yatafi, ita kuma ta shiga gida, hajiya zainu ta tsareta wai sai ta fadi inda taje, tunda ta kira anty tace, bata can. Bishira tace naje ba mijina da surukaina hakuri ne, hajiya zainu tace ni dazai maida ki ai sai nafi kowa murna. Na gaji da zamanki da

qazantarki, tunda babanku yaqi ki koma makaranta yakashe miki kudi ki goge ko kya samu mai kudin dazai aure ki, to gara kin koma can kin qarata. Abba kam shi tunaninshi ta ina zai soma sanar da ummi dawowar bishira? Don baya son ko kusa hankalinta yatashi, baya son wani abu yayi musu katsalandan a cikin daddadan zamansu, don haka ya share bai fada mata ba. Da dare alhaji da umma suka je, an sasanta sannan suka taho da alkawarin cewa gobe zata dawo dakinta. Washegari umma ta kira Abba tace ya share ma bishira daki yau zata dawo, yace umma nifa gsky dabata hankalina yafi kwanciya. Sannan ina ta tunanin yanda zan tunkari ummi da wannan zancen, umma ta riqe baki tare da rafka salati, yace ynzun tsoron ummin ka koma ne? Yace, a'a umma kin gata sakankance ynzun hankalinta yakwanta sai kuma taji nazo mata da zance dawowar bishira? Tace, shi kenan nina fada mata. Awaya ta kira ummi tafada mata cewa bishira zata dawo, duk datasan cewa matar mijinta ce dama, amma sai da gabanta yafadi. Umma taja mata kunne da cewa kada taji kada tagani, abba ranar sai kusan sha biyu zaije gurin aiki. Don haka yace kannanshi suje su soma fito da kayan kafin yazo sunzo sun fada ma ummi, ita ce ta bude musu dakunan don abba ya canza makulli bayan tafiyar bishira. Abba ya shigo tana zaune kan kujera sai tunani take yi na irin zaman dazasu yi in bishira tadawo. Yazauna tare dariko hannunta, tunanin me ki ke yi? Takalle shi, halin rayuwa nake tunani, yace yanzun umma ta kira ni jiya sun je gidan su bishira wai yau zata dawo. Ummi ta taba baki, Allah yakawo ta lpy. Ya ce ni ban soba gsky. Sbd ke ummi tadafa kirji, sbd ni? Ni ya abba, kada kasa duniya ta zage ni, Tare fa nasameku? Yace to ni dai kada kiga kamar da son raina, tace don Allah ya Abba kabar zancen nan. Kaje kagyar mata dakunanta don su kamal bazasu iya ba, yanufi gurinsu ganin kamar ya damu yasa itama taje tasa musu hannu don dai ya saki ranshi, sun gyara tsaf ummi ta goge sannan ta rufe dakin.

Har magriba bishira bata ji an ce za'a maida taba, sai ta dauki wayar kanwarta ta kira shi wai yazo don Allah yadauketa. Tsakanin mata da miji sai Allah, nan ya tausaya mata yace zaizo, kafin ya isa sai daya sai mata waya irin dai ta hannun ummi. Har cikin gidan ya shiga suka gaisa da babanta, yayi murna sosai yayi tawa Abba godiya, tare da ba shi hakuri yace yasan yanda ta horu zai gata canza da yardar Allah. Yasa aka turo ta yayi mata nasiha, sannan ya gargadeta da cewa inhar ta bari mijinta yakawa kararta zatayi mamakin abinda zai mata. Tace, insha Allahu baza ta kara ba, yakawo kudi yaba Abba, da kyar ya amsa ita kuma ya bata wasu zannuwa acikin leda, yace su raba da abokiya zamanta. Taje tayi wa hajiya zainu sallama suka tafi, tamkar baquwa haka ta koma, sai kace basu taba zaman aure da Abba ba, nauyinsa take ji. Suna tafe ya ciro waya ya miqa mata, tasa hannu ta amsa yace taki ce, tayi ta godiya yace ba komai. Sallamarsu tasa gaban ummi faduwa, ta dake ta fito ta amsa, wani kishi ya tasho mata amma saita danne. Ta kalli bishira tare dayi mata sannu dazuwa, ta amsa tana kallon ummi tayi kyau tagoge daga ka ganta kaga wayayya 'yar gatan miji. Ta dauko makullin dakin ta ba bishira, abba kuma ya nufi dakin ummi. Bishira ta dinga kallon yanda abba ya gyara gidan yaja gini ta gefen ummi yayi mata falo da kicin, sannan tsakar gidan an gyare shi da tiles. Haka bandakin su yagyara shi, nan dai bishira ta shiga dakinta ta zauna bakin gado tana yi wa allah godiya tare dayi wa kanta alkawarin har abada bazata ta kara yin yaji ko ta janyo abinda zaisa mijinta ya sake ta ba. Ummi tana kan gado tana karanta wani littafi yazo ya zauna bakin gadon bata ko kalle shi ba don haushi take ji. Sai take ganin kamar rawar kai yake yi da dawowar bishiran, kuma tuntuni yana zuwa gurin ta ya boye mata. Yace madam ina son in yi magana da ku ne ke da bishira, ummi tace ina jin ka, yace can zaki zo muje. Tace, gsky nagaji, kayi maganar da safe. Yagama gano kishi ne ke damunta, don haka yayi

murmushi yace yanda kikace hakan za'ayi. Ya fita kamar minti 30 yasake shigowa ya aje mata leda tare da cewa saida safe aciki tace Allah yabamu alheri. Yana tafiya taje ta banko kofarta, yau kam bacci ya qi idanun ummi sbd tayi sabon bacci a haqarqarin Abba. Dukkan filolinta ta rasa wanda zai maye mata madadin haqarqarin mijinta, ynzun yancan da wata tasan yanda yake wannan rawar jikin ynzun ya manta da batunta. Tarasa me yake mata dadi, littafin datake karantawa kuwa sam bata fahimtar abinda ke ciki. Hka ta dinga zubda hawaye har nisan dare, ganin bata da wata mafita, tashi tayi ta bude kofa lokacin 2 saura taje tayo alwala tazo ta kama nafila. Abba jin bude kofarta ne yasa shi leqowa ta window aranshi yaji tausayinta don yasan bata iya bacci sai ajikinshi, ita bata san ya leqo ba don ko hanyar dakin bata ishe ta kallo ba. Yakalli bishira wadda bacci yayi gaba da ita ya tausaya mata sosai yanda tayi tarawar jiki alokacin auratayyarsu dazun. Yadauko wayarshi yarubuta ma ummi sako. KI KWANTA KIYI BACCI BABY, TARE DA QISIMA CEWA KINA LAFE AMAKWANCINKI (WATO JIKINA) INA CIKE DA KEWAR LEBUNANKI. Tana sallah taji shigowar saqo amma bata yi ko marmarin dubawa ba, haka tai sallah har zuwa lokacin da bacci yasoma fizgarta. Tayi adduo'o'i sannan ta kwanta, saida asubahi ne datayi sallah sannan ta karanta, dan tsaki taja tare da cewa, Karya kawai, kishi yasa ta fadin haka don tasan Abba sosai baya boye mata komai ynzun. Sai dai abinda yasake qular da ita da asubahin nan yanda tana fita shi kuma ya fito wanka, duk da tasan dole wani abu yafaru tsakaninshi damatarsa, amma sai taga tamkar da gayya ya tsaya don tafito taganshi. Tna idar da sallah ta dora ruwa akicin dinta, tadafa ruwan tea taje kicin din bishira tadauko flask tazo ta wanke ta zuba musu ruwan zafi taje kofar bishira tayi sallama bishiran ce ta bude ummi tamiqa mata tare da cewa an tashi lpy? Cikin sakin fuska tace, lpy lau, nagode. Ummi ta ce ba komai takoma dakinta ta kulle kofarta don yau bata da darasin

safe. Abba ma yau bada wuri zai fita ba, don haka yadan samu baccin safe sai 8 yayi wanka ya karya, sannan yanufi dakin ummi. Kofarta tana rufe, ya kwankwasa ta share sai can dai dataji yaqi tafiya sannan tazo tabude. Takalle shiya yi kyau cikin kananan kaya, ta kauda kai tare da cewa, an tashi lpy? Yace lpy lau, kin karya? Tace, um'um sai anjima, zata rufe kofar yace, makaranta fa? Tace sai karfe 2 nake da darasi. Ta maida kofar ta rufe, yayi dan murmushin takaici sannan yafita. Kwananshi 2 dakin bishira yayi niyyar dawowa dakin ummi, don ya kosa yadawo ya lallasheta bazai iya daukar wannan shariyar da take mishiba. Tsakaninta da bishira lpy lau amma shi sai tana wani share shi. part 33 the end
Posted by Bashir Sani Fesan on 15 Dec 2016 - 14:45
Ya shigo da zumudi zai nufi dakinta, tamiqe cikin fara'a daga wanke-wanken da take yi ta amshi ledar hannunsa da jakar laptop ta nufi dakin bishira. Shida bishira suka bita da kallo, ganin zata shiga bishira tace ummi yau ai dakinki yake. Ummi tace injiwa? Anty bishara ai kullum ke ce dashi har sai kin rama duk kwanakin da kika dauka agida. Kinga kenan kusan wata goma sha daya kenan. Abba cikin sauri yace ke mahaukaciya ce? Ina ki kasamo wannan fatawar? Ta kalle shi, sannan tashiga dakin ta ajiye ta fito taqara kallonshi gurin malamai, yace to ban yarda ba, don haka zanci gaba dayi muku kwana bibbiyunku, ummi tace to ni na yafe mata nawa kwanakin bishira tace nagode ummi. Haushi ya cika Abba, amma shi bazai dauki wannan horon da ummi take shirin yi masa ba. Yadawo dakin bishira a fili yafurta kema saina baki haushi zakiyi dakin sanin wannan furucin. Sharewa yayi yaci gaba da kwana dakin bishira tare da nuna kulawa ga bishiran. Ummi ta jure duk da duk daren Allah sai taci kuka ta gode Allah, sannan tashiga zargin cewa shi ma ya Abban dama can yana son tarewa dakin bishira, inba haka bame zaisa yayi saurin yarda kuma yayi ta nuna mata soyayya? Ganin ummi tana yi tamkar bata damu ba yasa shi qa rajin haushi, yadawo da yamma suna

zaune kowa A qofarshi. Ummi tayi kwalliya cikin qananan kaya, bishira kuma tana sanye da leshi, karatun littafi bishiran keyi ita kuma ummi tana yin gyaran qumbunanta. Bawai suna wata hira bane amma suna kula juna sosai musamman bishira tana son su saba da ummi. Ummin ce bata cika son fitowa ba, bishira ta tashi ta masa sannu dazuwa tare da amsar kayan hannunsa don yanzun tana koyi da ummi gurin kyautatawa, ummi ta kalle shi sannu dazuwa, ya amsa da yauwa baby. Yakalli bishira sweety zanyi wanka, tace to, takai masa ruwa yashiga dakinta, sai tazo tace masa takai nan kuma yajanyo bishira jikinshi. Ba wai yana da bukata bane, amma don ya shaqar da ummi sai ya banko kofar, qaran kofar ne yasa ummi kallon gurin dakin. Ta duqar dakai taci gaba da abinda take yi, kusan minti arba'in suka fito, Abba ya matsawa bishira wai suyi wanka tare, tace ni bazan iya ba akwai ummi dama da dare ne inajin kunya. Kuma kada taga kamar cin fuska ne, yace kenan don kada ki bata mata rai ni mijinki bazaki faranta min ba ko? Dole ta bishi suka shiga bayi. Baqin ciki yasa ummi tashi tashige daki, kuka sosai tayi daga nan bata fito ba sai magriba, tanayin alwala tarufo kofa, washegari ma qin bude qofar tayi daga alwalar asubahi. Abba yayi ta raba ido ya ganta amma bata fito ba, yasan fushi take, ya kira wayarta taqi dagowa yayi mata saqo cewa in zata makaranta tafito inkuma sai darana ta bude ta amshi kudin mota. Tana gama karantawa tayi wuri da wayar ba tare data bashi amsa ba, haka ya tafi. Bishira ta qwanqwasa ma ummi ta bude suka gaisa, tace naga baki fito bane ina fata lpy? Tace lpy lau bacci ne, tace yau baza kije makaranta bane? Ummi tace, zanje sai sha biyu. Bishira tace kinji dadinki ni gashi nan ina tayi masa zancen karatun amma ya share ni, ummi tace inkin matsa zai yarda, tace ko za ki dan sa min baki? Ummi ta riqe baki, ni a wa? Ke da yake hannunki ai ke ce zai saurara, ni kin zo ne ma ki zage ni. Bishira tace wane irin zagi? Ni dama ki amshi mijinki ummi don gangar jikinshi ce kawai

agurina, amma ruhinsa yana gurinki. Ummi ta ce, ngd da zagi, bishira ta ce zancan gsky ne ba wani zagi. Haka suka yi ta rayuwa cikin kwanakin ummi kam har rama tayi shima Abba ya rage walwala don wanda yasan kan kula da shi kamarta. Yayi missing din abincinta. Amma ya gaji bazai jure ba. Ya tuna bishira tace masa zata ta yini gidan ummanshi. Don haka yana gama muhimman abubuwan da zai yi agurin aikin yanufi gida. Ummi tana shirin tafiya makaranta ta dauko jakarta sai kurum taga mutum kamar an jeho shi. Ta daure fuska tamkar bata taba dariya ba, yace ummi nagaji kin ji ko, na gaji da wannan horon naki. Laifin me nayi miki? In don na dawo da bishira ne sai in saketa, duk ba kece kika takura min sai na dawo da ita ba? Ummi tace, ni karka doran jakar tsaba kasa kaji su bini, ka saki matarka sbd ni? Ba ruwana. Yace, to ki dawo yanda kike, kuma ki janye batunki na wai kin haqura dani, niban haqura ba. Ke ma kuma nasan dole ki kasa kanki, ummi ta ce ni ban damu ba, ya ce qarya ne gashi nan duk kin rame? Ya canza daga fada zuwa lallashi, ummi don Allah na roqeki mu koma kamar da, haba bebyna. Ya lalubo hannunta ta qwace, don Allah ka tafi kada bishira ta dawo ta same ka anan ta zargi wani abu. Haushi yakamashi sosai, ya daga murya da qarfi, kin san Allah ummi zan hadaki da umma, ta nufi hanya fita, nikaga kada kasa ni yi latti don lokaci yayi nisa. Ya ficiko ta ta dawo ba zaki makarantar ba, ke an ma daina karatun tunda yafi ni. Ta zubar da jakar da hijabi ta nufi gado shi kuma ya fita cikin zafin rai, gidan su umma yaje. Bishira tana dakin umma tana sallah yabi umma kicin, umma gurinki nazo, ta dube shi lafiya Abba? Ya turo baki, alamun ranshi bace baki, yace umma ki sallami bishira, tace kamar yaya? Yace taje can gidan ko muyi maganar agabanta? Tace, kyale ta muje dakin babanku. Abba ya fada ma umma komai da ummi ke masa, tun dawowar bishira ran umma ya baci tace ka barni da ita. Banda shashancin ta da ita kadai take son azauna? Baga bishirar nan ba gidan nan ta gane

kuskurenta ko yau yarinyar nan sai da tace in yafe ta nace ni dama ban riqe ta da wani abu ba. Shine ita zata qirqiro fitina? Yace, umma ai ba da bishira take yi ba dani take yi, tace to zata gane kurenta da dare kuzo kai da ita. Umma ce ta kira ta awaya tace tazo ita da abba, jikinta ya mutu don tasan qararta aka kai, tana idar da sallar isha'i taje gidan. Can tasamu abba, nan ko umma ta rufe tada fada, koda tsohuwa ta jiyo tazo umma tafada mata komai sai ta shiga fada. Wai ai kishi halas ne, ke suwaiba tsakani ga Allah ko ke bazaki so kishiya ba, bare ita yarinya. Abba yace to gata nan ita ce fata dame ne nida batun in dawo da bishirar, yanzun na dawo da ita kuma ni abin ya qare akaina? Nan fa umma tayi mata tatas, ta kuma sata anan ta ba Abba Haquri, aka kira shi awaya ya fita. Umma ta samu dama taqara yi mata nasiha da cewa, in bnda shirmenki yaushe zaki bar ladanki, hanyar aljannarki kice kinyi fushi da ita kin barwa kishiya? To kada in sake jin haka, ki riqe darajarki da mijinki, ke ganinki da ita. Ta jima tana bata shawara kafin Abba yadawo suka nufi gida. Ya shiga gurin Bishira ya fada mata cewa yau gurin ummi zai kwana, nan ya bar ta da kewa yanufi gurin ummi, tamkar yaune daren farkonsu hara sukai rayuwa aranar. ** ** ** ** Kwanci tashi asarar mai rai, shekara ta zagayo lokacin bishira da tsohon ciki, Abba nason yara don muhibba taqi dawowa tafi son umma dole suka haqura suka bar mata. Ta haifi 'yarta budurwa tubarkalla ranar suna ta ci sunan sahura inda suka sa mata walida. Ummi nason yara, don haka in tana gida to tana manne da walida, Abba yana damuwa da rashin samun cikin ummi, wanda ita ummin ta barma Allah komai. Shekaru uku sun sake biyo baya, lokacin Bishira ta sake haihuwar habiba takwara Abba yayi wa ummi. Tsohuwa an qara tsufa, 'yan rigingimu sun qaru tace ita Abba yama takwara amma bata son ya duke ta irin yanda yayi wa ummi. Abba kullum qara son ummi yake, umma ta matsa masa sai da yayi qoqari ya sai fili rabin filoti tace kuma a rage ciye ciyen dadin nan agina

shì. Haka kuwa ya gina flat mai daki hudu, daya ummi daya bishira, sai nashi sannan na yara. Yayi qoqari gurin gyaran falon ita kuma ummi ya canza mata kayan daki don bishira an canza mata daza su tashi agidan su. Yace tabishi bashi in ya samu zai bata kudi amadadin kayan daya saima ummi, tace ta yafe. Ummi dake karantar (BUSSINESS) har ta hada (H.N.D) dinta kuma tayi bautar qasa. Abba dai yace baza'ayi aiki ba amma ya yarda tayi kasuwanci, Alhaji babba ne ya bata jari inda take saro kaya zannuwa, lesuna, takalma zuwa jakunkuna. Abin ya amsheta don har kayan aure tana hadawa, tana yin saqo irin su kwatano da chaina, india, pakistan ko dubai, ta hanyar wani wan kawarta. Haka kawai ummi ta samu kanta da zaban abinci, yawan bacci kasala da dai sauransu, sam bata san takamaiman lokacin al'adarta ba. Don bata wani lissafi in yazo shi kenan in bai zo ba bata damu ba tama cire ranta daga batun ciki. Abba ya kalli nonuwanta, baby kwanan nan kirjinki ya cika sosai, gashi kinyi haske ko kin canza mai ne? Tace yaya yaushe kazama likita? Yace, ummi kin fa canza shirya muje asibiti, ta ce ya Abba don Allah ka bar ni nagaji dazuwa asibiti. Yace, to ni zan je inya tambaya game da yanda ki ka canza. Cikin jin haushi tace sai ka dawo. Ga yara atsakar gida sun ishe mu, yace ni naki nake qawar in gani nasan addu'ar da nike yi bazata fadi kara banza ba, sannan ga qoqarin danake yi, shiru ta masa. Dagaske yake yi yaje yayi wa likita bayani, yace yadai kawo fitsarinta. Sai da suka yi tsiya da qyar bishira ta lallasheta ta yarda ta bada fitsarin. Rungume likitan yaya lokacin da yake fada masa ciki ne in dai har fitsarinta ne. Afalo gaban bishira da yara abba ya rungume ummi yana murna, ji tayi tamkar tsokana amma ganin ya zauna yana ta buga waya yanata yadawa ta amince cewa gske ne. Don haka ta tashi ta shiga dakinta tayi alwala tazo tayi nafila raka'a 2 cikin kuku take godewa Allah tare da addu'ar ya raba lpy. Ya bata mai albarka. Tsohuwa ma kuka ta saka lokacin da labarin ya

riske su. Ummi taga gata musamman daya kasance cikin yazo da kumburi tayi sumtum. Duk kowa ya tsorata sbd tunanin ko hawan jininta ne ya tashi. ALLAH cikin Ikonshi data tashi haihuwa saita santalo danta cikin gajeriyar nakuda, sak da abba kwabo da kwabo. Rungume ummi abba yayi don murna, sunan alhaji babba ya sake maida wa kuma walid din dai suke kiranshi. Watan yaron bakwai ummi ta sake rasa kanta, kuka wiwi ta dinga yi shiko abba murna kamar yayi rawa. Tasake samun da namiji inda yaci sunan alhaji karami suka sa masa hibban. Haka suka ci gaba da rayuwa cikin haquri da juna, tsakanin bishira da ummi, bama irin bishira saboda abba baya iya boye son ummi. Kan 'ya'yansu ahade ba kya gane bambanci, bishira ta gane umma uwa ce guda har da rabi, don haka hatta shawara saitaje gurin umma kuma ko sabani suka samu da abba gurin umma take zuwa. Ita kuma umma ta dauke ta babu bambanci da ummi, don bata taba fada ma ummi sirrin bishira ba. Sahura yanzun ta yarda umma da alhaji sune rufin asirinsu, kuma gatan Abba, bashi ma da yayi aure gidan dasu ummi suka tashi nan ya zauna. Dangin bishira yanzun sunga bishira ta samu natsuwa sun sulhunta. Abba agurin aikinshi yana ta samun ci gaba, lamuran sai godiya. Ummi tashafa addu'ar da takeyi sannan tamiqe tana linke dardumar tace kallon me ka ishe ni dashi ne ya Abba, yace ina kallo ne na kusan samun da na uku wannan karon takwara zan ma kaina. Ummi ta jefa masa dardumar hannunta, daina min fata ni, yace ban karanci likitanci ba amma ni likitanki ne. Ta fada kanshi, ya rike fuskarta yana kallonta cikin ido, ummi lokuta da yawa ina zama inta tuna da, musamman in na kalli 'yan yaranmu wadanda suke matuqar kama dani, tace me kafi tunawa a baya? Yace, yanda kikayi ta kirana awaya kina tsara ni suhaylan kaduna. Suka sa dariya. Ni kam nafi tuna yanda ni da kai muka yi ta 'ZURFIN CIKI' dason juna. Yace Allah yabarni da ke har abada matata. Ta kwantar da kanta amakwancinta "Amin mijina". Muma Allah ya bar

mu da masoyanmu har gidan aljanna, ya bamu lafiya dazama lafiya. Ya zaunar mana da 'yan uwanmu lafiya, Amin ya rabbi. ** ** ** ** Bayan shekara goma naje nasamu yaya Abba nace inason muhibba yace badamuwa yabani kyautar gida da mota. Ummi kuma ta hada mun kayan lefe saboda namijin kokarin danayi na rubuto maku wannan littafin aka daura mana aure da muhibbata muka tare muka cigaba da soyayya fiye dasu ummi ma.